01/01/2024

*INDA RAI*
*Part 3. Page 1*
NA
*Aysha Aliyu Garkuwa*

Gyara zamansa yayi tare da fesar da sassayan numfashi murya cike kamala da daraja ya fara motsa lips inshi cikin nusar wa yake maganar.
"Ita ƙaddara haka take juya fari ya koma baƙi, ko ta juya baƙi ya koma fari, haka Allah ke tsara abubuwa bi bayan bi, komai na faruwa tamkar yadda yake a ru babuce a lauhul Mahfouz, babu abin da ke sauya baƙar ƙaddara ta koma fara kamar kusantar Allah da addu'a mai cike da yaƙini da kuma tsananta wa wajan kiyaye dokokin Allah, haka babu rayuwa mai daɗi sama da bin Allah da manzon sa, kiyaye dukkan dokar Allah na saka hasken zuciya da kwarjini da arziƙi da ɗaukaka, ka bi Allah ka huta da masifar duniya, domin shi Allah ne ya ce kiyaye sallah na hana mutum aikata alfasha.
Ubangiji Allah ya ba mu ikon bin Allah sau da ƙafa."
Tajj ya ƙara sa yana rufe alƙur'anin da ya biya wa Laylah.
Cikin nutsuwa Laylah ta ta ce.
"Amin Amin."
Ta ƙare tana rufe nata Alkur'anin tana turawa Afisha abin wasanta.

Ishmah ce ta shigo da tirtsetsan cikinta tana wata iriyar tafiya kamar mai shirin faɗuwa ƙasa.

A hankali ta zauna muryarta na ɗan rawa ta ce.

"Ina zaton naƙuda ce....."

Da sauri ya miƙe ya tunkarota ya taimaka mata ta miƙe suka koma ɗaki.
Yana dubawa ya ga tabbas haihuwar ce, yana ƙoƙarin taimaka mata wajan saka kaya Addawa ta shigo a ƙagauce.

"Laylah ta ce min ta ji Ishmah na faɗin naƙuda ce..."

Cikin tashin hankali ya ce.

"Ita ce, asibitin za mu tafi yanzun nan."

Da sauri Addawa ta yo wajan Ishmah cikin kulawa.

"Sannu Ishmah, sannu kin ji daure, Ubangiji Allah ya raba lafiya, in Sha Allah cikin sauƙi za ki haihu kamar yadda kika haifi Afisha."

Da Addawa da Tajj ne suka taimaka mata dan ilahirin jikinta rawa yake haka ciwon murɗa mata yake sosai cikin jin azaba bayan sun shiga mota ta kasa daure ta na nishi ta ce.

"Wayyo Allah na Yah Afif wannan ciwo! Ya yi min yawa ya ilahil alamina ka sassauta min, dan Allah Sheykh ka yi min addu'a."
Sai kuma ta sauke Ajiyan zuciya tana fitar da wani irin nunfashi.

Idan ciwon ya lafa kuma sai gumi, da ya dawo sai ta ƙanƙame hannunta akan mararta tana nishin azaba jikinta na karkarwa ta ce.

"Allahumma la sahla illa ma ja'altahu sahlan wa anta taj'alul hazna iza shi'ita sahlan."

Sai ta fara nishin azabtar jin zafi.

Da wannan ciwon suka isa asibitin, Dr Farida da Sister Nuraini, ce suka amshe ta.

Shi kuwa Tajj yana can neman zam-zam ɗin sa daya tanada dan ya yi mata addu'a.

Sai da ya gama ya kawo mata har a lokacin tana nuƙurƙusar azaba dan har ƙwalla sai da ta yi, duk jikinsa ya mutu murus hak hankalinsa ya tashi dan bai taɓa ganinta cikin wahala irin yau ba.

Sai kusan bayan minti goma kana ta fara nishin da ke tabbatar da fitowar ɗa.

Da sauri ya sha mur ya ce Dr Farida da Nuraini su fita ya yi supporting ɗin matarsa.

Ala dole suka fice dan dama sun san a rina sun saba,

Cikin hukuncin Allah ta haihu ɗan yaron na fitowa wani ya ƙara fitowa mahaifarsu kuma ta zama ɗaya, sun tabbata Identical twins kenan.

Tuni kukansu ya karaɗe asibitin, nan da nan Tajj ya yanke musu cibi ya shinfiɗe su kan ƙirjin Ishmah yana murna da farin cikin baiwar Allah a kansa na ba shi duk abin da ya nema, da fari ya nemi Afisha Allah ya ba shi yanzu ya nemi ƴan biyu ga shi ya samu duk maza.

Ita kuwa Ishmah  duk da a gajiye take sai da ta ji tsananin farin cikin godiya ga Allah.

A lokacin da Tajj ya kuma yin sujudush shukur, a lokacin Dr Farida ta shigo tana cewa wallahi sai ta taimakawa Dr Ishmah ko me za a yi ayi, tana zuwa ya ɗebo yace ta gayawa dukkan ma'aikatan cikin asibitin tun daga kan Doctors har Nurses cewa zai ninka musu albashinsu na

wannan watar.  patients ɗin dake cikin Hospital ɗin kuma yau duk kyauta za'ayi musu komai.

Kowa cikin asibitin cike yake da murnan abin alherin da ya samu, kana bakunansu ɗauke da addu'ar Allah ya raya ya ƙara lafiya.

Ko da Laylah da Hamisu da Zulaihat da suka zo, dukkansu sun yi murna matuƙa.

Cikin jin daɗi Laylah ta ce.

"Ni ƴar gata, lokaci ɗaya na samu ƙanne maza har biyu ga Afisha ta kuma, alhamdulillah."

Hamisu kam matsowa yayi kusa da yayarta yana cewa.
"Ku dai rayuwa na yi muku kyau, Allah ya ƙara kyawun rayuwa a gaba, duk sanda kika tashi haihuwa anty Ishmah sai ki haifa mana kyawawan yaran da za su zama abun kallo da ta'ujibi a wajan kowa, gaskiya ƴan biyu suna da kyau, ga kama nan sak da Afisha." Murmushi tana tana kallonshi cikin son ɗan uwan nata da takeji duk Qatar bata da kamarsa.

Sai dare ta koma gida domin ƙalau take daga ita har yaran, Afisha da ta fara iya magana duk da ba sosai ake ganewa ba saboda tsamin baki irin na yara ganin kowa na murna itama ta fara murna tana ta nuna yaran tana magana.

"Amty lelah ce ta she kannena ne ko?"

Haka take ta faɗa tana nuna yaran tana murna.

Ko ta sunkuyar da kanta ta rinkayi karatun Qur'ani  tana tofa musu.

Tun a daren Tajj ya raɗa musu sunan da tun kafin a samu cikinsu suka yanke shawarar sa. Ayeed da Ayaan. Rahma da Dr Amdaz ma a cikin daren ya kawo ta dan ta yi tsalle ta dire akan ita fa dole ta zo ta yi wa anty Ishmah zaman wanka, daƙyar ya lallasheta akan kwana ɗaya za ta yi ta dawo dan ya ce sai dai shi da ita su je gidan su tare dan ƙafarsa ƙafar matarsa.

Ethiopia kuwa sosai yan uwa suka rinƙa farin ciki da samun yan tagwayen Tajj More especially team Arfah da Imran.

Hakama su Abba a Nigeria.

Ranar suna kam sun sha shagali duk lecture aka yi kamar wancan sai dai wannan an yi sa ne akan falalar aure da tara zuri'a.

Ma sha Allah walima ta yi walima an raba kyautuka yara sun sha addu'a da fatan tsawon rai da Kyakkyawar rayuwa.

Tun da akayi suna Hamisu ya ɗauki hoton Ayeed da Ayaan ya tura wa Arfah da Imran suke tsananin murna dan sai da Arfah ya tura group ɗin su na dangi ya ce Uncle ɗin su na can Allah na azurta shi da zuri'a masu albarka, haka kuma ya turawa Ya Abana yana faɗa masa idan ya kore shi, to Allah ya raya shi da zuri'a cikin ƙanƙanin lokaci haka dai rayuwa taci gaba da tafiya....

BAYAN SHEKARA BAKWAI.

Hall ne faffaɗan gaske, da ya haɗa manyan malaman musabaƙa na duniya.
Ko wacce ƙasa da wakilanta da kuma ɗalibanta wajan.
Kan mutane kowa ka gani cikin shiga ta kamala, dukkan wakilan gasar larabawa ne, gefe guda kuma manyan malamai ne da suke zaune Alqur'ani a gabansu suna kallo, can gefe kuma mutane tsagi-tsagi ke zaune ɓangaren maza dabam da na mata, haka gefen dama yara ne matasa masu kalolin uniform kala-kala.

Dukkansu sun yi shiru suna saurararan Ayeed da yake karatun musabaƙa, yana gamawa wajan ya ɗauki kabbara, kana aka fara kiran sunayen ƴan hizfi talatin, sunan makarantar su Afisha ne a farko kuma makarantar ce zata waƙilci musabaƙar Duniya baki ɗaya da za'ayu a ƙasar tasu na Qatar.
Dalilin da ya sa aka fara kiranta dan ita ta wakilci makarantar ta su.

Cikin nutsuwa Kyakkyawar yarinyar yar matashiyar mai kimanin shekaru 8 da yan watanni a duniya ta tashi sanye cikin Kyakkyawar shiga mai kamala uwa uba haiba da ƙwarjinta, a nutse ta hau kan mimbari kana ta zauna bisa kujerar da aka tanadar musu, cikin ɗan taradadi ta zubawa malamin da ke jan aya ido  dan ta fara gabatar da nata karatun.

Cikin ƙwarewa malamin ya fara da Bismillah kana ya karanto tsakiyar suratul shu'ara'i.

Yana ajiye wa ta buɗe zazzaƙar muryarta da A'uziyya da bissimillah ta fara karatun cikin wata ƙira'a mai fusgar hankalin da saka  nutsuwar mai saurarontaa da kuma kamanceceniya data mahaifinta saidai banbancin muryarta na mace kuma da yarinta.

Tajj da ke zaune a cikin masu sauraro, tun da aka ambaci sunanta gabansa ya faɗi duk da yana da confidence akanta, lokacin da ta fara ƙira'ar ya ji sautin muryarta na yarinta da kuma zaƙi sai ya kwantar da kansa jikin kujerar ya lumshe ido yana jin sanyin daɗi da annushuwa kana zuciyarsa na bin karatun cikin tabbatarwa kansa tana yin karatun dai-dai. Yanayin shirun wajan da yadda duk al'ummar wajan suka bada ƙaimi wajan sauraron Afisha ya sanyaya masa rai da ƙara masa daɗi ainun a cikin ransa.

Ita kuwa Ishmah, da hannunta ke riƙe yake da ƙaramar yarinyar ta da ta haifa Fatima suke ce mata Daddey hankalinta ne ya kwanta tare da ƙurawa alƙalan ido tana kallon yadda suke gyaɗa kai cike da nutsuwa da kuma kwanciyar hankalin yadda karatun nata ke fita harafi bayan harafi. Hawayen farin ciki ya yi kwance saman idanuwanta, zuciyarta na harbawa ranta ya yi mata fari ƙal, haka jefi-jefi tana kallon alƙalan cikin annushuwa da yadda jikinsu ya bayyana gamsuwa da karatun Afisha dan sai jinjina kai suke cike da fuskar nuna gamsuwa.

Malamin ne ya sake janyo aya a cikin suratul Namli, nam ma ba ta yi ƙasa a gwiwa ba, ta ɗauki karatun tamkar a cikin ƙwaƙwalwarta ta zana, harafin na fita dai-dai, haka babu algus a wajan fitar da gunna da jan harka, da bayar da lamunin dai-dai-ta kowanne Ikfa'i Idgami, Iƙlabi, tamkir da tafkeer, cikin lokaci ƙalilan ta saye duk mutanen wajan da dadɗan karatunta na shigar zuciya da sa sanyi a zukatan masu sauraro mafiya yawa hawaye ke cika mazauna wurin ido.

Wani daga cikin malaman ne ya sake katse ta ya ɗauko suratul Ƙamar, har da Fathi da Gafir, dama wasu surorin dukkan surorin nan babu wata sura da harafinta ko tajweedin ta ya ɓace mata, ta biya su daidai.

A haka aka sallame ta.

Nan hankalin Tajj ya kwanta yadda ya ji kabbarar manyan malamai, nutsuwa da wani tsantsan farin ciki na ratsa shi bisa baiwa da ni'imar Allah a gare sa, haƙiƙa samun ta a matsayin ƴa babbar ni'ima ce, wannan kaɗai ya ishe sa wannan kaɗai ya gama masa jin daɗin duniya har da na lahira.  Shi kam yana jinsa tamkar ɗan gata a wajan Allah ga shi ya azurta shi ta mar'atussaliha ga kuma ƴaƴa nagari wanda su Allah ya kira ƙawar duniya, sai ya sauke numfashi yana hamdala da hailala bisa babbar ni'imar da ya samu.

A haka ka yi ta yi har aka zo kan su Laylah ƴan hizfi hamsin, itama ta yi namijin ƙoƙari domin ta saka shi cikin nishaɗin da Afisha ta tsunduma shi duk da dai su team ɗin Chaina sun basu wuta da wuya in basu dokesu ba.

Sanarwar da ake yi tasa ya ɗaga kai yana sauraro.
"A yau muka kawo ƙarshen wannan musabaƙar, in Sha Allah zuwa anjima za a ji sakamakon idan mun tattara makin muna yi wa kowa fatan alkairi. Sannan bisa sabon doka iyaye za su koma gida, za a raka ƴaƴan su har gida da sakamon da suka samu, muna yi wa kowa fatan alkairi."

Bayan angama sun ta so a hanya ya yi ta saka musu albarka har yana ƙwallar farin ciki Ishmah kam sai waya takeyi da yan uwanta da tuni Hamisu ya tura musu.
Shi kuwa Tajj tuni yayi  gayyatar masu decorations houses, domin yana da tsammanin ƴaƴansa na da nasara.

Kafin su je har masu decorations ɗin sun hallara sun fara aikinsu tuƙuru, cikin ƙanƙanin lokaci suka gama kana ya yi ordern special cake na taya ƴaƴan sa murna da kuma sauran kyautukan

da ya saya dan ya ƙarfafa musu gwiwa musamman su Ayid da yaune suke cika shekaru bakwai cib cib.

A nutse suke a falo sun zubawa tv ido duk jikinsu na azarɓaɓin jin sakamakon gasar. Jefi-jefi yana duba media, dan gaba ɗaya media ta cika da vedios ɗin Afisha na karatu mutane nata faɗin amazing voice, dan murya ce gare ta ta yara mai ratsa zuciya da salon karatu mai fusgar hankalin mai sauraro, wasu da yawa na faɗin karatun ya tsuma su ta yadda har suka kasa riƙe hawayensu, suna kuma addu'ar Allah ya sa ita za ta cinye tuni ake ta haɗa video'nta dana babanta.

Yabon su da ƙarfafawar su ta kwantar masa da hankali dan yana zaune sai murmushi yake yana girgiza kai, yana da tabbacin nan gaba Afisha za ta yi ɗaukaka ta ban mamaki akan ƙira'a.

Ya rasa me ya sa ba a sanar da sakamakon ba da wuri, duk sun bi sun ruɗar shi, kwatsam ya jiyo muryarsu cikin sautin murna da zaƙuwa cikin rakaɗi ya jiyo muryar Afisha.

"Alhamdulillah bini'imatahi ta tummussalihun! Abeyna! I'm the winner!!!""

Ta faɗa tun daga farfajiyar gidan cikin ɗaga murya, a guje ta shigo falon Ayeed na binta a baya shi ma yana cewa.

"Ni ma na cinye."

Da sauri Tajj ya ɗan miƙe daga kishingiɗen da ya yi akan kujera.
Idonsa ya lumshe kana cikin sanyi da sauƙaƙawa ya ce. "Alhamdulillah."

Ya kuma buɗe ido, zuciyarsa na luguden farin ciki, kana ya ce.

"Ma sha Allah, congratulation yarana masu tsananin albarka."
Ya ƙare mgnar yana buɗa musu hannunsa.

Faɗa wa jikinsa suka yi cikin murnar.
Rungume su tayi tsam kamar zai maidasu cikinsa.

Laylah ta shigo hannunta riƙe da Ayaan da fuskarsa take a turɓune, ita kuma tana ta lallashinsa.

Afisha ta kalle shi ta ce.

"Abeyna albishirinka, na zo ta ɗaya!"

Ayeed ya tare ta da cewar.

"Ni kuma a hizfi goma, shi kuma Ayaan yana ɓata rai ne dan ya zo a na biyu."

Cikin tsananin ɓacin rai Ayaan ya ce.

"Ka ji wannan Ayeed ɗin abin da da rabin maki ka wuce ni, kuma ai ma, son kai aka yi."

Sai ya yi shiru yana ajiyar zuciya.

Ishmah ce ta janyo sa jikinta ta fara lallashinsa, zuciyarta tamkar wacca aka yi wa babban albishir

"Ka yi haƙuri, ai kaga kaine ka cinye a na hadis, kuma yanzu aka fara, sannan kace da rabin maki ya wuce ka ko?"

Ɗaga kai ya yi cikin sanyin jiki kana ya ce.

"Kuma ma, komai rabo ne da ƙaddara haka Allah ya tsara Ayeed ne na ɗaya ni ma ina yi wa kaina fatan alkairi Allah ya sa ina da rabo a gaba idan Allah ya rayar da mu."

Dukansu tsura masa ido suka yi saboda Ayaan a nutse yake magana kamar ba yaro ba, idan ya yi wani furucin sai ka rantse koya masa shi aka yi.

Murmushi Tajj ya yi ya ce.

"In Sha Allah ɗan albarka, ai kai mai nasara ne, kuma dukkanku za ku ci gaba da nasara a rayuwarku in Sha Allah."
Ya ƙare mgnar yana haɗasu duka a jikinsa yana kallon Laylah data
zauna tana sakin ajiyar zuciya.

"Ni ma fa nina nazo mana ta biyu a hizfi hamsin."

Kallonta Tajj ya yi ya ce.

"Ai dole na cike miki 60 ɗin nan Laylah kada ki gajiyar da ni akan sauke shi, har yanzu ba ki haɗa sittin ba, haba ta gaban goshina zan dage kafin ki cika shekaru ashirin dai ki cike settin cib."

Na rai na rai ta yi da ido sai kuma ta ce.

"Allah Abeyna ina iya bakin ƙoƙarina a kan hakan ai an kusa in Sha Allah Amman fa dudu wata shida ne ya rage in cika shekaru ashirin ɗin fa."

Cikin yaƙini Tajj yace.
“In sha Allah kafin nan kin cikace settin”.
Ayeed ne ya miƙe ya fara tsalle yana karatun Alqur'ani cikin ƙwarewa.

"Abeyna, Allah anty Laylah ta ci ka wasa, sai ka haɗa mata da bulala.."

Hamisu ne ya shigo yana kabbara.

"Congratulation to me,  duka kyawawan yarana ne suka yi nasara a gasar karatun Alkur'ani na Qatar duk media da gari sun ɗauka ga matar ma anyi ƙoƙarin ai Yah Afif da cike settin da cike shekaru ashirin da haɗe digree da ɗaura aurenmu duk a rana ɗaya za'ayi su ko."

Da sauri Laylah ta rufe ido.
Tajj kuwa cikin farin ciki yace.
“In sha Allah kuwa haka za'ayi."
Ishmah kuwa ruggume Laylah tayi cike da farin cikin haɗin ta sa Hamisu.
Shi kuwa Hamisu wani irin murmushi mai cike da farin ciki yakeyi.

Da gudu Ayeed ya tafi ya rungume sa yana dariya.

"Sosai ma duk mu muka yi nasara Uncle Hamisu. Anty Afisha na ɗaya a hizfi talatin da tafsir, anty Laylah na biyu a hizfi hamsin Ayaan na biyu..."

Sai ya kalli Ayaan da ya ke kwance jikin Ishmah yana kallonsa shi ma.

Shafa kansa Ishmah ta yi ta ce.

"Ai shi ya fara ci a na hadisi kai kuma ka zo na biyu, yanzu kuma ka zo na ɗaya ya zo na biyu shi kenan anyi balance equetion."
Shi kuwa Tajj wayoyinsu dana Ishmah ke ta ƙarar shigowar message ɗin abokan arziƙi na taya su murnan wannan abun farin ciki.

Zama Hamisu ya yi ya ce wa Tajj.

"Malamansu fa suna falon waje suna jiranka."

Cikin mamaki Tajj da Ishmah suka kalli yaran.

Laylah ta kama baki ta ce.

"Laaaa! Mantawa na yi, Ayaan me ya sa baka tuna mun ba."

Ayaan ya ƙara kwanciya jikin mamnsa ya ce.

"Taɓ! Ni ma mancewa na yi tare mu ke da su."

Afisha ce ta kwashe da dariya ta ce.

"Kowa na murna ina ma za ka tuna da su, ai ni tun da akace nice wacca ta cinye na ke da burin zuwa na faɗa wa Abeyna."

Ayeed da yake ta tsalle-tsallen murna ya ce.

"Ni kam ma na mance da  kowa sai farin ciki."

A ɗan hanzarce Tajj ya miƙe yana faɗin.

"Dukkanku dai Allah ya yi muku albarka, ku shiga ciki ku faɗa wa Addawa dan jiranku take ta yi tun ɗazu."

Ya fice dan ganawa da malamansu.

A cikin nutsuwa ya shiga suka gaisa cikin girmamawa dan suna matuƙar girmama shi.

Cikin nutsuwa shugaban makarantar ya fara magana.

"Alhamdulillah, kamar yadda aka tsara an gama gasa lafiya yaranka su ne suka yi nasara makaranta da mu kanmu muna alfahari da hakan, kuma mun zo yi maka murna da kuma kawo musu kyautukan da suka samu."

Sauke numfashi Tajj ya yi yana jin zuciyarsa wasai kamar an wanke ta tass da babu sauran wani datti.

"Alhamdulillah, Allah mun gode maka, na gode sosai Sheikh Khalilullah, Allah ya sa ka da alkairi."

Murmushi suka kana ɗayan ya ce.

"Ai mu ne da yin godiya, domin dai ba dan jajircewarka ba, tabbas da makarantar mu ba ta yi sunan da a yanzu ta yi ba, kaga dalilin yaranka kowa zai  so kawo yaransa makarantar, ai mu tsakaninmu da kai sai addu'a dan mun san bawai iyakar karantarwar mu bane harda jajircewarka da bitarsu a gida."

Cikin tsananin farin ciki

Suka miƙa dan nuna wa Tajj kyautukan, bayan motar su fall cike da kaya kala-kala dan dukkansu sun samu kaya masu yawa.

Cikin tsananin murna Tajj ya amshi kyautukan amma banda kuɗi ya ce malaman su riƙe, suka ce sam babu wannan zancan da ƙyar dai suka daidaita akan sai dai a raba kuɗin biyu su ɗau ɗaya ya ɗauki ɗaya kana ga kwaitar kujerar hajji wa Afisha.

Lokacin da suke jigilar shigar da kayan cikin gida zuciyar Tajj sai haske da farin ciki take yau Allah ya nuna masa ranar da zuri'arsa ta sama masa farin cikin zamowa ƙololuwa a harkar Alqur'ani.

Ita kanta Ishmah saddar da kanta ƙasa ta yi tana ƙoƙarin mayar da ƙwallar da ta taru cikin idanuwanta.

Hotunan da Laylah ta ɗauka lokacin ba su kyautuka ta turawa Arfah da yake ta faman yi mata magiya akan ta yi wa Allah ta tura masa hoton Afishansa na amsar kyautar gwarzuwa a karatun Alkur'ani, tana turawa ya ce ta makaro domin tuni ya samu vedios ɗin a media dan yanzu babu inda vedion karatunta bai je ba a duniya.

Ethiopia.
Shi kenan yanzu ruwa yana ƙoƙarin karewa ɗan kada? Ya Abana ya faɗa yana kallon hotunan da Arfah ya turo masa wai ƴaƴan Tajj sun yi nasarar zama gwarazan hafizai.

Ya sauke numfashi yana kallon Afisha da ta buɗe baki tana amsar awards sai ya lumshe ido yana jin azababbiyar soyayarta kana ya buɗe vedion karatunta.

Lokacin da ta zo ayar ta biyun ƙarshe cikin suratul yaseen innama amruhu iza arada shai'an an ya ƙulu lahu kun fayakum.

Sai ya lumshe idonsa yana jin zazzaƙar muryarta cikin nata salon karatun da ƙira'ar mai ɗaukan hankali.

Ban da yana kallon lasifikan da bakinta tabbas da ya ce, wannan karatun nata, sai da aka kai shi computer aka gyara saboda daɗinsa da yadda yake kwantar da hankali.

Alƙalin gasar ne ya ƙara janyo mata aya a cikin suratul shu'ara'i nan ma ta ɗauke tamkar wata na'ura ta fara biyawa cikin gwaninta da ƙwarewa.

Cikin tsananin jin daɗi da son kusanci da yarinyar
Ya sake lumshe ido yana jin karatun zuciyarsa na kwaɗaita masa son ta da ƙaunarta.

Lokacin da ta gama sai ya ƙara dawo da vedion farko ya ci gaba da sauraren ta yana lumshe ido.

Shi kam Tajj rayuwarsa ta yi kyau, duk da baya tare dani Allah ya albarkace shi ta inda ban yi tsammani ba, samun zuri'a irin wannan babbar kyauta ce daga Allah wannan kuma baya rasa nasaba da riƙo da Alqur'ani mai girma da bin tafarkin dai-dai.

Sai kuma ya buɗe lumsassun idanunsa. Yanq ji wani irin tsananin farin ciki na ratsa shi, ya saki murmushi kana ya miƙe, ya na kokarin kiran waya, cikin mintina biyu aka ɗaga ya ce.

"A saye ƙaton Sa babba yanzu a kawo a yanka shi a yi lafiyayyan abinci a soya naman a bayar sadaka muyi kiyafa."
Ya faɗa cikin bada ubarni
Ya kashe yana jin wannan sadakar ta yi kaɗan dan nunawa Ubangijin sa farincikinsa ga ni'imar da yayi masa a cikin zuriyarsa, fitowa ya yi waje, masu zama ƙofar gidansa ya hau rabawa kuɗi cikin fara'a da jan su a wasa, kana ya bi dukkan ƴaƴansa da alert ɗin bank dan shi bai san wane kalar daɗi yake ji na a cikin ransa, abin da ya sani duk ya tuna da zaƙin Muryar Afisha da yadda take karatu sai ya ji zai iya bayar da komi nasa dan farin cikin kasancewarta jikarsa.

Ƴaƴansa kam sun yi mamaki matuƙa don har tambayar junansu suka dinka yi akan sauyin ya Abana da kuma kyautarsa ta ban mamaki a ranar.

Washegari ma haka ya farka cikin farin ciki, kana ya ci gaba da sauraron karatun da ke sanyaya masa rai da korar da ƙuncin cikin ransa.

A hankali gabansa ya faɗi da ya tuna waskataccan mafarkin da ya yi jiya wanda ya zame masa masifa, a kodayaushe dai mafarkin ne ke ta nanata kansa.

Cikin jurewa takaicinsa akan rayuwarsa ta yanzu ya miƙe yana tunanin kai ziyarar bazata asibiti dan haka kawai hankalinsa ke karkato masa shi.

Driver ya kira ya shiga ya fashi umarnin su tafi asibitin ko Allah zai sa ya ci karo da wani abun da zai haska masa abinda ke faruwa a asibitin duk da har yanzu sautin ƙira'ar Afisha na kai komo cikin kunnuwansa shi ya taimaka wajen tabbatar da farin cikin sa a zuciyarsa, a hankali ya ɗauko wayarsa ya kunna karatun yana gyaɗa kansa cikin jin alfaharin jikarsa ce ke wannan karatun tamkar ƴar larabawa mai na'ura a cikin maƙogoro.

Tun daga bakin asibitin ya fara cin karo da abun mamaki, domin wayam ya gan shi babu

mutane, ya sani yanzu babu patients sosai dan kuɗin shiga na asibitin da ka so sittin cikin ɗari babu, wani zubin a aljihunsa ake cikawa Doctors ɗin kuɗin albashi yana kawo hakan da yadda yanzu mutane ke matuƙar kulawa da kawunansu wajan gujewa cin ko yin wani abu da zai saka su cikin wata lalura.

Bai tsinke ba sai da ya shiga farfajiyar asibitin, tamkar wanda aka yi kora, kai tsaye wards ya shiga babu patients sai wasu da ba su fi mutum biyar ba, takaici ya sa ya runtse ido yana hasko shekarun baya lokacin da Afif ke kula da asibitin.

D asauri ya buɗe idonsa ya shiga ɓangaren office ɗin Doctors ɗin wasu a rufe har sun yi yana cikin mamaki ya kira wani Nurse da ya zo wucewa.

"Dan Allah Ina doctors ɗin nan suke."

Wani irin kallo ya yi masa kana ya ce.

"Amma kai baƙo ne ko nace ka jima baka shigo asibitin nan ba, ai ko ni da ban daɗe ba, ban zo na same su ba, kawai office ɗin fanko ne babu kowa a ciki."

Har ya juya zai tafi ya dakatar da shi.

"Dan Allah dana tsaya na tambaye ka."

Cikin ƙaguwa ya tsaya.

"Ka yi sauri ka tambaye ni don ina da aikin yi."

"To korarsu aka yi ko me ya sa suka bar asibitin alhali nasan da Asibitin nan ba baya ba wajan kula da majinyaci."

Kallonsa Nurse ɗin ya yi kana ya gyaɗa kai.

"Ada Kam a yanzu mai asibitin kamar taɓi-taɓi haka yake, babu mutunci lamarinsa, don yau zai ɗauke ka aiki, da kaga kuskure ka yi masa gyara sai ya ce baka isa ba ya baka sallama ko kuma ya tattara albashinmu na wata biyar ya hana, daga baya sai ya baka na wata ɗaya ya ce zai cika maka sauran, ba ma wannan ba, babu ingantattun kayan aiki ko nagartaccan maganin daya dace....
Kash bai kamata na faɗa maka haka ba, amma gaskkiya ɗaya ce, ni ma nan jira nake na samu wani asibitin na koma can dan ba zan iya ba...."
Yana kaiwa na ya juya ya tafi.

Bango Malam ya dafa kana ya sulale ya durƙushe kan kujerar dake gefenshi dan yana da tabbacin ba zai iya jure tsayuwar nan ba dan tabbas zai iya yanke jiki ya yi mummunan faɗuwa.

Gabansa na falfala faɗuwa haka zuciyarsa na ƙara hasa wutar baƙin ciki da takaicin wannan al'amari.

Sai da ya kwashe kusan minti goma kana ya lallashi zuciyarsa ya miƙe ya yi injection room, babu kowa, labor room nan ma mace ɗaya ya gani da ya tambaye ta  ta ce su biyu ne kacal, ita da wacca take aikin dare, yanzu babu ma'aikata, sai ya wuce sauran rooms ɗin nan ma duk sammakal.

Da sauri ya koma mota ya ce wa driver ya tsaya a waje har sai ya kira shi.

Yana shiga ya fashe da kuka, rabonsa da kuka irin wannan tun yana matashin saurayi.

Kuka ya yi yana dafe zuciyarsa cikin ƙunci da ɗacin rai.

"Kabiru ne ko Aryan?  Waya cuce ni a cikinsu?" Sai ya dafe kai ya ci gaba da kukan mai sauti.

"Haka rayuwata zata ƙare cikin baƙar ƙaddara yara su yi ta zalunta ta suna yaudarata, na ɗora su akan tafarkin Allah su watsa min ƙasa a ido, su cutar da ni, Yah Allah na tuba menene na yi wanda wannan masifa take bibiyata a yanzu? Me na aikata?"

Sai ya kuma fashe wa da kuka, cikin kukan ya ci gaba da magana.

"Iya sanina ban taɓa zaluntar kowa ba amma me ya sa ni ake zaluntata kuma masu zaluncin yarana na cikina?".

Wayarsa ya ciro hannunsa na karkarwa ya kira Aryan.

Bata jima ba tana ringing ya ɗaga.

Sai da ya yi ƙoƙari matuƙa wajan saita kansa kana ya ce.

"Aryan ya Asibiti kuwa yana nan dai komai na tafiya ƙalau."

Muryar Aryan ɗin ta karaɗe kunnuwansa.

"Sosai kusa Ya Abana asibiti na nan yadda ake so, ina kula maka da shi da Kabirun ma yanzu kam sai hamdala."

Cikin cijewa da takaici ya kashe wayar yana ƙara fashewa da kuka.

Lallai ba ƙaramin masifa ba ce wannan Allah ya jarabce ka da ƴaƴa irin nasa Aryan da Kabiru masu son ganin bayansa.
"Allah na tu ba nasan Tajj bazai taɓa haintata hakaba koda kwatankwacin hakaba".

Dole ya yi kuka mai sauti dan rage raɗaɗin bakin cikin munafurtarsa da ƴaƴan cikinsa suka yi Sai kuma ya saki tattausan murmushi tunowa da Afisha lokaci ɗaya kaso tamanin na baƙin cikinsa ya fice daga zuciyarsa sa bege da son ganin ahlin Tajj ɗin suka cike mishi gurbin da zumuɗi da maraji ji yake dole ya kasance gaban Afishan dasu Ayeed suji ɗuminsa a matsayin kanku, cikin farin ciki ya goge ƙwallar kana ya ƙara dai-dai-ta kansa sannan ya kira Driver ya zo su tafi.

A kan hanya karatun Afisha ya kunna ya lumshe ido yana saurare zuciyarsa na raya masa samun ta kaɗai matsayin jika ya ishe sa duk da irin mummunan zaluncin da ƴaƴan cikinsa ke yi masa.

Zaune yake a falonsa yayinda duk manyan yaransa ke zaune hakama matansa.
Cikin tura baki Arfah da Imran da tuni yanzu sun zana cikakkun pillots masu kamala.
"Nifa sauri nake zan fita, dan ina da parsingers ɗin Pakistan.".
Arfah ya faɗa yana miƙewa tsaye.
Imran ma miƙewar yayi tare da cewa.
"Ni kuwa da tun juya da dare ina saman gajumare sai yanzu da na iso zan huta kuma ka wani kiramu kuma kaƙi cewa komai".
Da sauri suka koma zaune saboda ganin kallon da Yah Hafiz yake musu.
Shi kuwa Yah Abana E passport ɗinsa ya miƙewa Arfah tare da juyowa ya kalli Ummey cikin tsuke fuska da yace.
"Kuje da Arfah ki bashi E passport ɗinki.
Kai kuma Arfah ka kaiwa Siddiq mun gama mgna dashi zai samo mana sahalewar barin ƙasar nan".
Cikin sauri ya kuma tsuke fuska tare da yin kici-kici da ita ya watsawa Mom Amal wani irin kallon rufe min baki sabida jin tana cewa.
"Barin ƙasar kuma? To kuma ina zakuje? Kuma ai ma wannan karon ba tafiyarta bace".
Cikin sauri Ummu Aryan tace.
"Ni tafiyatace kuma nasan Malam bazaiyi hakan a wofiba.
Allah ya kaiku lfy ya dawo daku lfy yasa ayi Umrah karɓeɓɓe, ni na yafe duniya da ƙiyama dama mun gama magana da Malam ɗazu da rana".

Wani irin kallon tashin hankali Aryan ke yiwa Yah Abana tare da cewa.
“Toh Yah Abana? Umaran kenan zaku tafi?”.
Yana miƙewa tsaye yace.
“Inda ka aikeni”.
Murmushi Hajia Babba maman su Yah Hafiz kenan tayi tare da miƙewa tana kallon Ummeey tace.
“Ni dai dama zam-zam ɗina ya ƙare in kunje ki kawo mana da yawa”.
Ita kam Ummey sai binsu da ido takeyi cike da aminci yarda dasu a kanta duk da tasan wannan karon bada ita zaije Umaran ba kamar yadda yake binsu layi layi amman tayi farin ciki da tafiyar ko ba komai zata ƙara samun daman kai kukanta ga mai kowa mai komai.
Ita kuwa Ummey tare suka fita da Arfah.
Shi kuwa Yah Abana Imran ya kira suka shige har can uwar ɗakansa.

Mom Amal kuwa da sauri ta fice Aryan da Kabiru na biye da ita a baya.

Ganin shiru-shuru Yah Abana da Imran basu fito bane yasa duk su Yah Hafiz suka watse.

Washe gari da yamma Arfah ne ke kwance a masauƙinsa a Pakistan yana waya da Imran cikin tarin ɗaurwar kai yake cewa.
“Oga Siddiq dai yace min ya gama musu komai na tafiyar jibi jirginsu zai tashi.”.
Cikin sauri Imran yace.
“To wai ina zasu kebe?”.
Kai Arfah ya ɗan mirgina tare da cewa.
“Ohon masa ni dai ban tambaya ba kuma ma ai kaima kasan bazai wuce Umrah zai je yi ba.
Numfashi mai sarƙafe da nazari Imran ya sauƙe kana sukayi sallama...

Wajan cike yake maƙil da mutane haka gefe jojis ne da ke zauna kan manyan kujeru suna kallon mai gabatar da rawar wata yarinya Najisa, banda shewa da kida da kuma rawar da yarinyar ke yi babu abin da ke ta shi a wajan, sai da ta gama aka yi mata shewa da tafi jojis ɗin suka tambaye ta sunanta da kuma burinta akan nasarar da idan ta yi.

Can gefe Adaya ce da Yasir da ta saka masa wasu shegun fitinannan kaya, sai ƙura masa ido da ta yi cikin ƙarfafa masa gwiwa.

Sauke numfashi ta yi a hankali kana ta ɗauke fuska ta ce.

"Wannan ita ce ranar da na jima ina zumuɗi da saurare, Yasir ka cika min burina, Yasir ka zama kaine gwarzon wannan gasar kamar yadda na zama gwarzuwa a dukkan gasar rawa ta duniya."

Izzin ne ya katse ta.

"Duk yadda za a yi Yasir a yi ka yi nasara, burin mu ace ka yi gadon mamanka na zama gwani na gwanaye."

Sai ya waiwayo ya kalli Asina.
Ya ce.
"Kina da abin cewa."

Sunkuyawa Asina ta yi ta ce.
"Yasir mamanka tun kana jariri ta ɗau alwashin zamowarka gwani, dan Allah ka cika mata burinta kada ka ji gazawa kasawa, ka ƙarfafa kanka za ka zama gwani in sha Allah kuma bayan ka cinye gwajin yau dole duniya tasan sunanka da mahaifinka yake fata da burin ka fito duniya ta sanka dashi."

Gyaɗa kansa ya yi ya kalli lasifikan da take kiran sunansa dan gabatar da rawar sa zagaye na ƙarshe wanda daga shi sai faɗin result.

Cikin wata tafiya da Izzin ya koya masa ya tunkaro wajan, tafiyar da ta tafi da imanin mutanen wajan suka saka sowa, kana wasu na ƙara zuzuta kyawunsa da haibar yaron yana zuwa aka miƙa masa lasifika domin amsa tambayoyi kafin ya fara rawar.

Ɗaya daga cikin jojis ɗin ne ya ce.

"Kyakkyawan yaronmu menene burinka idan ka samu nasarar cin gasar nan?"

Shiru Yasir ya yi yana kallon mutanen wajan yana jin tsananin farin ciki da zaƙuwa wajan cikama mamansa burinta na zamowarsa gwarzon rawa.

Cikin zazzaƙar muryarsa ya ce.

"Ina son gina gidan koyar da rawa na yara irina, sannan ina son na zama babban ɗan rawa da babu kamar sa a duniya kamar yadda mamana ta zama ƴar rawa na duniya!"

By
*GARKUWAR MARUBUTA**INDA RAI*
Part 3 page 2
Na
*Aysha Aliyu Garkuwa*

Wajan ne ya ɗauki shewa, da tafi.
Lokaci ɗaya jojis ɗin suka ba shi umarni ya fara  gabatar da rawar gwaji dan fitar da gwani, wanda zai wakilci ƙasar su gasar rawar yara ta duniya da za'ayi a Dubai.

Cikin salo na ɗaukan hankali ya fara karairaya jikinsa tamkar babu ƙashi, tuni suka fara ihu da ta'ujjibi hatta jojis ɗin mamaki suke suna sai sare ido suke tare da buɗe baki suna kallon ikon Allah.

Tun da ya fara rawar wajan ya ruɗe matuƙa fiye da yadda aka ruɗewa sauran abokanansa na fidda gwanayen da zasu wakilci tawargar gasar rawar.

Ganin ihun da kuma nuna yadda ya birge su ya ƙara masa ƙaimi wajan yin wasu salon rawar da ba a saba gani ba musamman a wajan yara irinsa, tuni mutane suka miƙe tsaye suna tafi wasu na tsalle suna kiran sunansa.
Yasir! Yasir!! Yasir!!!!!!
Tun kafin lokacinsa ya cika jojis uku suka danna masa likes  wajan ya ƙara ruɗewa wanda ke da tabbacin ya haye matakin gaba tabbacin dashi za'a wuce Dubai.

Lokaci na cika ya tsaya cikin salon rawar da sai da mutane suka bushe da dariya sai kuma ya juya ya fuskanci jojis ɗin tare da ɗaura hannunsa na dama kan ƙirjinsa gefen hagu kana ya ɗan sunkuyo alamun gaisuwa da girmama a yarensu na yan rawa.

Kana ya koma wajansa cike da tafiyar alfahari da jin ƙasaita domin ya san ya gama cinye wannan ɓangaren.

Washe gari.  QATAR.
Gidan cike yake da mutanen arziƙi masu zuwa sam barka, da taya su murnar lashe gasar karatun Alkur'ani da yaran gidan suka yi musamman Afisha da acikin awanni ƙalilan vedios ɗin ta ya ƙaraɗe media.

Rahma na zaune kusa da Ishma hannunta riƙe da yaranta ƴanbiyu, maza Shuraim da Shu'aib Dr Farida da yarinyar ta  Amani, da kuma yaron ciki da take da shi, sai Sister Nuraini da kuma sauran maƙotansu.

Ƴar ƙaramar walima aka yi ta murnar nasarar da suka samu kana aka yi rabon gift na al'qura'anil kareem da sauran hadisai da kuma ƙira'ar Afisha da ta yi kamar yadda babanta ya yi, tun daga falaƙi har Kahf, cikin zazzaƙar muryarta, tuntuni ta yi, ya bari ne sai bayan sun gama gasar ya fitar da karatunta, haka suka gama kowa ya watse bayan hotuna da vedios da aka yi mata.

Ishmah ce ta ƙwace wayarta a hannun ƙaramar yarinyar ta  Daddey da take ta tura ta a baki, tana goge wayar kiran Arfah ya shigo, sai da ta yi murmushi kana ta ɗaga cikin jin kewarsa.

"Arfah, fatan kana lafiya.?"

Dariyarsa ta ji cikin muryarsa ta matasan maza ma su ji da kansu.

"Ammeyna, fatan kowa na lafiya har rabin raina Afisha."

Ɗan murmushi ne ya kufce mata ta gyaɗa kai cikin gamsuwa.

"Mutuniyarka tana lafiya, amma wanna son kai da yawa ya ke, kullum dai Afisha babu maganar Ayan da Ayeed balle ƙaramar alhaki Daddey na duk ko kara baka min....."

Katse ta ya yi.

"Ana zancan rabin rai waya ke ta alewar zuciya?"

Dariya suka yi dukkansu.

"Afisha rabin raina ce, su kuma sweetheart ne kaɗai, kin ga banbancin bayyananne ne."

Afisha ce ta zo kusa da ita ba tare da ta sani ba.

"Ammeyna ki faɗa wa Ayeed ya daina taɓa min laptop, dan ai ba tashi ba ce."

Karaf Arfah ya ce.

"Yauwa Ammeynmu dan Allah bawa Afisha waya, sai na gama da ita kana zan miki murnar nasarar da muka samu, na gani a media ana ta magana akan My happiness harda masu cewa suna sonta Basu san Yah Arfah ya riga su ba."

Miƙa wa Afisha waya ta yi tana cewa.

"To me ya sa ya taɓa miki taki alhali shi ma yana da tashi?"

Amsar wayar ta yi ta kara a kunnanta.

"Assalamu alaikum warahmatullah wabarakatuhu."

Ya amsa cikin zakwaɗi kana ya ce.

"Kyale shi rabin raina idan ma laptop dubu kike so zan saya miki ai tunda kin cika mana

burinmu kin zama shahararriya a ɓangaren karatun Alkur'ani mai girma, ina taya ki murna alfaharin danginmu, ina miki fatan alkairi nan gaba ki zamo gwarzuwa a na hizfi sittin."

Dariya da kyau ta yi kana cikin son shi da sabawa da shi ta ce.

"Amin yayanmu Arfah, Allah ya saka da alkairi ya cika maka burinka."

Sai kuma tai maza ta miƙa wa Ishmah wayar tana ta dariya.

Dariya Ishmah ta yi ta ce.

"Irin wannan washe baki haka."

Muryar Arfah taji yana cewa.
"Ba dole ba tunda tana waya da rabin ranta."

Girgiza kai Ishmah ta yi kana ta ce.

"To, rabin ran juna, Allah ya saka da alkairi dai."
Amin yace tare da ɗaurawa da cewa
"Yanzu fa, Afisha kaɗan ya rage ta kai babanta jama'a a duniya, kinga kuwa yadda media ta ɗauka cikin ƙanƙanin lokaci, sai haɗa vedios ɗin karatunta ake yi dana babanta ana comparison, abin dai sai wanda ya gani."

Cikin jin dadi Ishmah ta ce.

"Na gani nima, gaskiya na yi mamakin wanzuwar karatun cikin ƙanƙanin lokaci, domin cikin awa ashirin da hudu zancan ya ƙaraɗe duniya, ƙanwar Yah Arfah kam Allah Ubangiji ya ƙarawa rayuwa al'barka."

Cikin jin daɗi Arfah ya ce.

"Amin Ammeynmu, matar Sheikh Tajj Afif, mahaifiyar Sheikhiya Afisha, gaskiya ki godewa Allah duk ke kaɗai wannan baiwa ga surku Arfah surutacce ga ƙani Hamisu mai mutunci."

Ranta ne ya yi mata tass kana ta sauke numfashi a hankali, bayan ta lumshe idonta cikin son yaron tace.
"Alhamdulillah Arfah, kullum cikin godiya muke ga Allah."

Kamar yadda take jin daɗin shi ma haka yake ji dan tana jiyo sautin muryarsa yadda ta fallasa sirrin ransa.
"To, Ammeynmu, sai mun sake magana dan yau ina da passingers duk da ba nisa zan yi ba."

Ɗan kwantar da kanta ta yi tan gyara zaman Amnah a kan cinyarta.
"To, Arfah Allah ya yi jagora sai na ji ka."

Asina ce ruggume da Yasir dake bacci cike da farin ciki, ido ta zubawa Adaya dake zaune tasa boron kayansa da ta gama haɗa masa komai na tafiyarsu da zasu yi gobe jumma'a zuwa Dubai jibi da safe za'a fara fafatawa.
Hankalinta duk na kan wayarta  cikin cikowar hawaye ta ɗago idanunta tare da kallon Asina murya cike da takaici tace.
“Asina wai meyasa wasu mutanen duniya basa son yan rawane, duk abinda zamuyi bazamu burgesu ba, kigafa yadda wasu keta tsine mana a comments wai mun lalace kuma munzo shima Yasir zamu lalata shi.
Sai kuma ta kalli Asina da tai kwaffa tare da cewa.
“Ni tsoro na ma kada tsinuwar da mutane suke mishi ta kamashi”.
Sai kuma duk suka juyo suka kalli Mamin Adayan data shigo tare da watsa musu mugun harara.
“Ai gsky mutane ke faɗa muku, sam baku maida Yasir abin so ko ƙauna bare alfahari dashi ba in dai a wurin mutanen kirki bane kuma lokacin nadama nan tafe gareku”.
Tura baki Adaya tayi tare da maida kallonta bisa wayarta.
Video gaba ta taurawa ido wanda Afisha ke tsaye tsakiyar malaman da duniya ke ji sasu a babin Alkur'ani mai girma tana raira karatu tamkar wacce akewa wahayinsa.
Cikin ƙarfin mu'ujizar Alkur'ani ta kasa wucewa.
Koda video ya ƙare bata wuceba Saida ya sake daga forko haka tai takallonsa har sau uku sai kuma ana huɗun ta shiga bin comments ɗin mutane ya Salam.
Shine abinda ta faɗa wanda yasa Asina kwantar da Yasir tazo suna kallon tare comments na forko kan video cewa yace.
“Alhamdulillah wannan itace abar alfaharinmu mutanen Ethiopia ba irinsu Adaya da Yasir ba”.
Da sauri ta kalli na ƙasanshi da wani ke cewa.
“Wannan ɗin itama yar Ethiopia ce”.
Da sauri wani balaraben Qatar yace.
“A'a wannan ƴar Qatar ce”.
Kusan mutun dari ne suka bawa wannan balaben amsa da cewa.
“A'a wannan asalinta yar Ethiopia ce, in ma bai sani ba to ya sani yaji sunanta mana Fatima Afif Tajj, shi kuwa Sheykh Afif Tajj ai kowa ya sani a duniya shi ɗan Ethiopia ne.”
Emojis sin murmushi da alamun so mafiya yawa suka rinƙa turowa sai kuma wani daga cikin larabawan Qatar yace.
“Amman ai raininmu ce”.
Da sauri Hamisu dake bibiyar duk Comments ɗin a video da sakan yace
“A'a duk ma ba taku bace, tamu ce ta Nigeria.”
Cikin sauri wani Balaraben Jordan yace.
“A'a kam wannan batai kalar kuba”.
Murmushi Sheykh Afif ɗin dake bibiyar Handel ɗin Hamisu wanda komai nasu Afisha dama shi kanshi Tajj din a handil nasa ake gani, cikin hikima da iya sarrafa harshe ih zuwa alƙalami yace.

“Afisha ta dukkan musulman duniya ne, duk inda kake in dai kai musulmine in Kai na mijine kai yayantane ko babanta ko ƙaninta in macece ke yayartace ko ƙanwarta ko Auntynta. Duk ƙasashen musulmai ita tasuce. Nigeria kuwa itace jigon raininta da tarbiyarta.
Ethiopia kuma itace tushenta jintan. Qatar kuma itace Mahaifarta kuma makarantar ta.
Yah salam kan wannan comment ɗin nashi an mishi like yafi 1.5m dan yasa dukkan musulmai jin farin ciki.
Hamisu kuwa da sauri yayi falon inda Afishan ke zaune tana yiwa Daddey bita.
Jawota yayi tare da cewa
“My dear zo nan kiyi video kiyi godiya ga masoyanki na fadin duniya.”
Cikin murmushi tace.
“To My Uncle”.
Ishmah kuwa murmushi tayi tare da miƙewa da nufi kitchen tana cewa.
“Ku dai kula sabida baki in yayi yawa da illa”.
Da sauri Addawa tace.
“Mu da muke da Alqur'ani mai girma ai baki baida wurin sauƙa a jikinta”.
Da sauri Laylah dake fitowa daga ɗakin Ishmah tace.
“Sosai ma kuwa Addawa mu kam badai mutumba sai Allah”.
Murmushi Ishmah tayi cikin gamsuwa da in sha Allah ba abinda baki zai musu tunda sun lizamci karatun Alkur'ani mai girma”.
Shi kam Hamisu sakin video yayi tare da komawa kan comments ɗin ganin Arfah yayi comments kan na Sheikh Afif da cewa.
“Uncle Tajj ka manta baka gaya musu cewa.
mijinta ɗaya ne a duniya kuma Yah Arfah ta ne so kowa ya kama kansa”.
Murmushi Afif yayi tare da cewa.
“Toh ai ka faɗa”.
Da sauri Hamisu yace.
“To in dai fa kana so ka ƙara min biyayya”.
Alamun dariya Imran ya tura tare da ƙarawa da cewa.
“Ai Uncle Hamisu dole muyi mubaya'a tunda muna son Afisha da Minnat ni, yanzu hakama ina shirin tafiya Nigeria ne.
Daga nan kuma sai duk suka bar TikTok ɗin suka koma Whatsapp group ɗinsu inda suke hirarsu.

Wani irin nannauyan numfashi Adayan ta fesar tare da ƙurawa sunan Tajj ido.
Sai kuma  ta kalli Asina tare da cewa.
“Mutumin nan kamarfa gasa yakeyi damu, kin tuna lokacin da muke kan gasarmuma kullum dashi ake mana misali ana kushemu, Kinga yanzu kuma da wannan beautiful baby ɗinsa yake daƙushe mana taurarin Yasir ɗinmu ana mana misali da ita”.
Da sauri suka kalli Umminta jin tana murmushi mai sauri tare da cewa.
"Ai ko a gaban Allah ya fiku, kuma yarsa ta fi ɗanku kuma bakuma kai yayi gasa da kuba, shi bai ma san da ruwan tsironku ba”.
Tana ƙare mgnar ta juya zata fita sai kuma ta tsaya tare da juyowa ta kallesu tace.
“Af nafa mance shegen yaron nan Izzin ne yazo yana waje.

Kuyi sauri ku sallameshi kafin Abpu ku ya fito".
Tana faɗin haka ta fice

Asina kuwa numfashi mai nauyi ta fesar tare da cewa.
"Barshi mu bashi nan da kwana biyar da za'ayi gasar nan, in sha Allah har abadan sunansa bazai sake tasiri ko daraja ko kima a duniyaba daga abun so zai zama abun ƙyama, dan ko jiya shine tattaunawar da mukayi da my Man".
Cikin sauri Adaya tace.
"To Amman meyasa kikaƙi ki gaya min tsarin naku".
Cikin yarda da kai tace.
"Kar ki damu nafi son sai naga Yasir yaci gasar zan gaya miki kafin nayi abin".
Cikin takaici Adayan tace.
In kinga dama ma karki gaya min."
Ta ƙare mgnar ta janta suka fita suka tafi.

Sai kuma ta ƙali part ɗin Abpu da sauri tare da cewa.
"Ke yi sauri mu fita kin san Abpu tunda ya samu Ify in Izzin yazo gidanan ji yake kamar ya hau kanshi da mota".
Murmushi Asina tayi tare da cewa.
"Nima in ya ganni kamar ya harbeni fa".
Cikin yin ƙasa da murya tace.
"Nima ko gaisuwata fa baya amsawa".
Daga nan suka fice suka tafi.

Ya Abana ne ya ƙurawa Afisha ido kamar mai son haddace fuskarta cikin sonta ya sa yatsansa akan play ɗin vedion nan da nan sautin muryarta ya bayyana Wanda hakan ya tilasta shi sakin ajiyar zuciya cikin wani irin yanayi, ya lumshe ido yana jin daɗin ƙira'ar.

A haka bgajeran bacci mai nauyi ya fisge shi.

Mom Amal ce ta shigo ɗakin nasa hannunta rike da fruts da ta yanko ta kawo masa, tun daga falonsa ta fara jiyo sautin karatun, cikin rawar jiki da tsananin faɗuwar gaba ta ajiye fruts ɗin ta sunkuya ta leƙa fuskarsa taga yana bacci da sauri ta ɗauki wayar da take a dai-dai kunnansa, cikin mamaki da ruɗewa take kallon fuskar Afisha.

"Ita ce."
Ta faɗa zuciyarta na rawa haka ɓacin ranta ya fito ɓaro-baro, da sauri ta katse karatun kana ta fara ƙoƙarin deleting vedion cikin rashin sanin abin yi, gab da za ta goge ta ji gyaran muryarsa.

Da sauri tsoron zuciyarta ya taka mata burki, ta saki ajiyar zuciya tana jin kamar ta fashe da kuka dan bakin ciki.

Cikin nannauyan baccinsa ya daina jin ƙira'ar da yake jinta tamkar tana wanke masa wani datti a cikin ƙwaƙwalwarsa, cikin mamaki da tarin gajiya ya buɗe ido tare da gyaran murya yana kallonta.

Kamar wata shashasha haka ta saki baki tana lashe leɓenta da yake a bushe, sai ta zauna kusa da shi cikin mutuwar jiki tana son fassara kallon da ya ke jifanta da shi, kamar wata mutum mutumi haka ta sadaƙar tare da ajiye wayar tana sunke kai cikin yanayin ƙunci da damuwa miƙewa yayi tare da shigewa baruwanta jim kaɗan ya fito bisa alama alwala yayi.
Cikin inda inda tace.
“Niko Malam yaushene tafiyar taku?”.
Da sauri tayi ƙasa da kanta saboda ganin wani irin futinennen kallon fahimtar sirrin zuciya da tunanin ƙwaƙwalwar kanta”.
Kabbara ya tayar ba tare da yace mata komai ba.

Ummeey ce zaune tare dasu Rashida harma da Halima wacce yau kwananta biyar kenan da zuwa.
Binafa ce ɗiyar Zakiya ke bisa cinyar  Ummey cikin tsananin jin daɗi suke kallon Video Afisha dasu Ayeed.
“Kai Allah na gode maka bisa ni'imar da kaimin da samun yara irinku da jikakiki kamar yaranku, Amman tabbas mahaifinku ya tauye min farin cikin rayuwata daya nesantani da ɗana da yaransa, ina son in ganni gani gasu Afishan Ayeed da Ayaan in ruggume Daddey kamar yadda nake ruggume da Binafa haka”.
Cikin rauni suke kallon fuskar ta dake zubda hawaye, sai kuma sukayi saurin kallon Imran da Hamida dake shigo Hamida na cewa.
“Ke da akayiwa shigel ɗin layin zuwa Umrah dan a ɗan rage Miki raɗaɗin rashin Uncle Tajj kuma shine kika tara mana Auntys ɗinmu a gaba zaki sasu kuka.”
Daƙuwa Maryam tayi mata.
Rashida kuwa murmushi tayi ganin Ummeynsu tayi murmushin tare da goge hawayenta.
Cikin wasa irin na yan auta da iyayensu Zakiya tace.
“Ato nima dai haka na gani su Ummey amare”.
Ɗan duka ta kaiwa Zakiya tare da miƙewa ta bar wurin.

Washe gari ranar juma'a.
Misalin ƙarfe tara na safe.
Meymey ce durƙushe gaban mahaifinta da mahaifiyarta.
Wani irin maraitacccen kuka mai cike da dana sani da nadama takeyi kuka ne mai tsananin ciwo da zogi da radaɗi takeyi har numfashinta na yayyankewa.
Yayinda shima Uncle Jibiril ɗin hawayene suke malala a kuma tunsa tare da danne sheshsheƙan kukan.
Mommy ta kuwa kukan takeyi harda majina.
Sai kuma ta kalli Meymey dake rarrafowa ta matso kusa da iyayen nata da kyau cikin

disashewar murya da rawan baki tace.
“Ya ku iyayena ku gafarceni, musamman ke Mommy da kikayi ta ƙoƙarin ganin kin fidda rashin gaskiyata a lokacin da nake ƙullawa Yah Afif wannan sharrin da ƙazafin da nayi masa, Amman son Zuciyata da ɗaurin gindin son da Abbana kemin ya hanaki samun damar bayyana makircina, gashi a sannu duniya da sakayyar Yah Afif tasa yau ni da kaina na zauna na baku labarin ƙazafin da nayi mishi”.
Sai kuma muryarta ta sarƙafe saboda tasowar wani sabon kuka.
Zuwa yanzu shima Uncle Jibiril kukan ya kwafce mishi cikin sauri kuma ya haɗiye kukan jin Meymey na tari tare dacewa.
“Dan Allah Mommy keda Abba ku rakani gidan Yah Abana in tonawa kaina da kaina asiri in bashi haƙuri in nemi gafararsa, ko Allah zai kawo min sauƙin wannan cutar damuwa da son aure wata ƙil in Yah Afif ya yafe min in samu mijin aure.”
Cikin tsanani ƙunar rai Mommy ta miƙe tsaye tare da nuna ƙirjinta da yatsarta manuniya.
“Har abadan bazan taɓa rakaki gidan Malam dan ki tonawa kanki asari basu Mom Amal makiran wofi dan ni idona da kunya kuma Zuciyata da tsoron Allah, so ke da kikayi amanki ke kaɗai lokacin da kikayi ban saniba kuma dan haka ke kaɗai zakije, kuma wallahi a yau ɗin nan zakije yanzun nan ma ba da jimawa ba.”
Sai kuma ta koma da baya ta faɗi zaune bisa kujera cikin kuka tace.
“Meymey kin shiga uku ina zaki kai zunubin raba uwa da ɗanta ke ba mutuwaba, Meymey ina zaki kai zunubin yiwa tsarkakekken mutum mahadaccin Alkur'ani ƙazafin zina da farraƙashi da iyayensa, Meymey ina zaki kai zunubin zubda hawayen Hajia Fatima Mahaifiyar Afif ina zaki kai zunubin sa mahadaccin Alkur'ani mai girma zubda hawayen. Shekara tarafa cib kenan kika rabashi da kowa nasa, ina zaki kai zunubin fidda tsiraici mutum mai kunya da kima da daraja.”
Sai kuma kawai ta fashe da kuka tare da cewa.
“Ta ya zakiyi tunanin samun salama a rayuwarki kinsa marainiyar Allah Laylah a wahala”.
Da sauri ta rarrafa ta koma gaban Abban nata cikin tsananin kuka tace.
“Abban dan Allah ka cewa Mommy tayi haƙuri ku rakani”.
Da sauri ta saki wani irin maraitacccen ƙara saboda jin sauƙan marin da Abban nata ya sake mata abinda bai taɓa yi mataba iya tsawon rayuwarsa.
“Kin cuceni Meymey kin ha'inci yardar da nayi Miki, kin farraƙa tsakanina da aminina Malam Muhammad,  Haba! Haba!! Haba!!! Ashe ba banza tunda abin ya faru Muhammad ya janye jikinsa dani, ba yadda banyiba alaƙarmu ta koma kamar yadda take a baya.
Amman abin yaci tura ya zama nine kawai ke binsa, daga baya na fahimci kamar baya son alaƙa dani dole tasa na ɗan ja baya dashi, sai muyi wata biyar bamuga junaba mutumin da da ko  wata ɗaya bamayi bamuga junaba, ashe jikinsa ne ya basa ɗiyata makirace”.
Sai kuma ya nuna mata hanyar fita cikin tsawa da bada umarni yace.
“Maza yanzu nan ba da jimawa ba.
Fice ki tafi kije ki lashe aman da kikayi, koda bazai yafe Miki keba nasan zai yafewa ɗansa kuma zai dawo dashi cikin ahlinsa wata ƙil kya samu ronggomin zunubin fice kije ki tonawa kanki asiri”.
Cikin tsoron fusatar mahaifin nata da gigicewa ta miƙe ta fita.

Shi kuwa a baya ya bita tare da bawa driver umarnin ya kaita gidan Malam Muhammad.

Qatar
Da sauri Afisha ta miƙe tsaye sabida jin wayar  Telephone ɗin su dake asalin main parlor nasu nata ringing.
Bisa alamu ba kowa.
Cikin ɗan sassarfanta da kuzarinta ta fito falon tana isewo wayar na katsewa.
Sai kuma ta juyo da sauri jin Addawa na cewa.
"Wake kira?".
 Kai ta ɗan jujjuya tare da cewa.
"Kiran ya katse wata ƙil Abeey nane".
Sai kuma duk suka juyo jin Hamisu da Laylah suna shigowa Ayeed da na biye dasu a baya.
Nan suka zube a falon.
Numfashi mai sanyi Laylah ta fesar kana ta zuƙo ƙamshin girkin Ishmah dake tashi bisa alamu tana kitchen ne.
Da sauri ta miƙe tana kallon Hamisu tare da cewa.
"Baby bari inje in taya Ammeyn aiki".
Cikin sauri shima ya miƙe tsaye tare da cewa.
"Muje tare".
Cikin kulawa da shaƙuwa mai dan ƙare da tsananin so tace.
 "Please Baby ka huta kullum aikin office baya barinka ka huta, yau weekend ɗinma kuma kace tare za'a shiga kitchen da kai, kawai ka huta gaya min me kake son in dafa maka".
Wani irin amintaccen kallon so yayi mata tare da cewa.
"To ai dama shi weekend ɗinma ana yinsa ne dan a bawa maza damar sakewa da matansu".
Da sauri Addawa tace.
"To ai ba'ayi aurenba tukuna ko Oga Hamisu".
Cike da kunya duk sukayi kitchen ɗin da sauri.
Dai-dai lokacin kuma kiran ya ƙara shigowa.
"Afisha amsa kiran kiji waye ne".
Da sauri ta miƙe tsaye tare da ɗaukar wayar tana kallon Ayeed da Ayaan dake game a System ɗin Laylah da ta ajiye yanzu.
"Aunty Laylah gasu Ayeed nan sun ritsa Miki System ɗin ki".
Ta faɗa tare da kai wayar kunnenta gami da yin sallama.
Ayeed kuwa da Ayaan harara suka banka mata tare da komawa kan 3 sitter suka zauna Ayeed na cewa.
"To uwar gulma ai ta sani".

Ita kuwa Afisha sallama ta kuma yi a karo na biyu dan jin ba'a amsa na forkonba.
Cikin wani irin matsanancin farincin da zama mabayyani a kan fuskarsa ya lumshe idanunsa cikin tsananin son yarinyar da ƙaunarsa da jin akwai tsananin sa'a da ƙarfin jini tunda gashi itace ma ta amsa kiransa duk da yawan mutanen gidan nasu.
Cikin son yarinyar da jin bai taɓa son wata ɗiya a duniya kwatankwacin son da yake mataba cikin Muryar dake nuna sonta yace.

“Wa'alaikumussalam warahamatullah ta'ala wa barkatuhu.
Afisha”.
Cikin rakaɗin ta da kuma zaƙin muryarta tace.
“Na'am”.
Cikin yanayin jin dadi yace.
“Ina Abbanki”.
Da sauri tace.
“Ina yini”.
Galala haka Ummey ta saki baki tana kallon Yah Abana cike da tsananin mamaki! Kaɗuwa! gami da sakewar tunaninta yau tunda jirginsu ya taso suka bar Ethiopia tun lokacin take cikin tsananin mamaki saboda jin sanarwar da akeyi musu kafin shiga jirgi ana faɗin su parsingers Qatar ne.
Bata gama sinkewa ba sai lokacin da taga jirginsu ya dira cikin babban birnin Qatar wato Doha. Har lau bata gama fahimtar komai ba a zatonta da tunaninta ko daga nan jirgin zasu ɗauki wasu parsingers ɗin da zasu wuce Sadia ne dasu kamar yadda kowa yake zaton Umrah Yah Abana zai tafi da Ummey.
Sai kuma taga sun wuce Hotel inda kanta ya ƙara kullewa.
Lissafin ta kuma ya gama sakewa yanzu da taji yana waya da Afisha.
Shi yasa ta kasa rufe bakinta bare idonta.

Cikin sanyi yace.
“Lfiya Lau Alhamdulillah Afisha my happiness. Ina Abbanki”.
Cikin jin son muryar mutumin da take waya da shi ɗin tace.
“Kai waye ne kake ta tambayar Abbana”.
Cikin jin zaƙuwar bayyana matsayinsa gareta yace.
“Suna Muhammad Tajjudden.
Abban Abbanki Afif Muhammad Tajj. Kakanki”.
Cikin mamaki irin ta yarinta ta zaro idanunta tare da yin Murmushi mai sauti tace.
“Kakana yana Nigeria ai, Abban Ammeyna, shi yake kiran mu a waya.”.
Da sauri yace.
“Nima kakanki ne Afisha Ni kakanki ne ke dasu Arfah dasu Imran na Ethiopia kin sansu ai”.
Kamar tana gabanshi ta gyaɗa kai tare da cewa.
“Eh na sansu mana shima Yah Abana Yah Arfah na nuna mana shi a waya, kuma ina son ganinsa. Abeey na kuma yace in ya kaimu wai zai ja mishi Allah ya isa. shiyasa bazamu taɓa ganinshi har abada, saboda baya son fushin Yah Abana ya sameshi”.
Da sauri ya rumtse idanunsa da ƙarfi tare da fesar da zazzafan numfashi murya cike da tarin ƙuna yace.
“Bawa mamanki waya”.
Da sauri ta juya ta kalli Addawa sai kuma ta ɗaga muryanta da ƙarfi tare da fara kiran Ishmah.
“Ammey! Ammey!! Ammeeyyy!!! Kizo”.
Da sauri Ishmah dasu Laylah da Hamisu duk suka fito.
Addawa kuwa ido ta zuba mata tana son nazartar kalamanta cikin sauri ta fara yafito Ishmah tana cewa.

“Ammey zo ki amshi waya wai kakana ne na Ethiopia wai yace shi Abban Abeey nane. Wai Yah Abana ne.
Ammeey kuma ina sonshi ina son ganinsa”.
Cikin sauri Ishmah ta amshi wayar tare da karata a kunne gami da sallama.
Tabbas tasan muryar Yah Abana kuma duk inda ta jita zata shaidata shiysa ta ganeshi da sauri ta ɗan rusunar da kanta tare da zamewa ta zauna bisa hannun kujerar dake gefenta cikin girmamawa tace.
“Barka da safiya Yah Abana”.
Wani irin zazzafan numfashi ya fesar tare da cewa.
“Barka dai Mamana ya gida dasu Afishana”.
Wani irin Ni'imataccen murmushi mai cike da mamaki tayi tare da cewa.
“Alhamdulillah duk muna lfy Yah Abana yasu Ummeey dasu Zakeeya”.
Sai kuma ta dubawa Addawa ido ganin yadda ta cika da matsanancin mamaki, kaɗuwa, kai harma da ruɗani”.
Ita kuwa Ishmah kai ta jinjina tare da cewa.
“Eh Yah Abana ina jinka”.
Gyaran murya yayi cikin sanyi yace.
“Yanzu haka ina cikin Qatar, ina 7 star hotel room 101. Ina neman alfarma in zan samu. Ina son ganin Afisha in zan samu kiyi haƙuri ki kawo min ita ko ki turo min ita kiyi min wannan alfarmar Mamana”.
Cikin sauri Ishmah ta fara jujjuya kanta yayinda tuni idanunta sun cika da hawaye har sun fara gangarowa kan kuncinta murya cike da rauni gami da girmamawa tace.
“Yah Abana Umarnin zaka bani ba alfarma ta zaka nemaba, Yah Afif da ni da yaranmu duk ai malakinka ne, Yah Abana ka bani umarni kawai ni kuwa zan bishi da yardar Allah”.
Cikin gamsuwa da tarbiyyarta yace.
“To mamana akawo Amin Afisha yanzu ina jira”.
Cikin girmamawa tace.
"To Yah Abana yanzu ƙanina Hamisu zai kawota”.
Cikin kallon Ummey yace.
"Allah ya Miki albakar”

“Amin Ya Allah”.
Ta ƙare mgnar tare da kallon wayar jin ya katse kiran.
Da sauri ta miƙe tsaye yayinda Addawa ta miƙe tsaye tanayi mata kallon neman ƙarin bayani.
Afisha cikin farin ciki take gayawa su Ayeed yau tayi magana da Yah Abana.

Da sauri Ishmah ta ruƙo hannayen Addawa cikin tabbatar tace.
“Allah mai iko maiyin yadda yaso a lokacin da yaso.
Addawa Yah Abana ne ya kira, kuma yace min yana nan cikin Qatar yana masauƙinsa nan kusa da muma hotel ɗin yake, kuma ya nemi alfarma a kai mishi Afisha”.
Ta ƙare mgnar cikin mabayyanin farin cikin da yasa hawayenta kuma zubowa.
Ita kuwa Afisha da sauri ta kamo hannun Laylah da itama idonta ya ciko da ƙwalla cikin tsananin jin daɗi take tsalle tana faɗin.

“Aunty Laylah kimin wanka ki shiryani Uncle Hamisu zai kaini wurin Yah Abana”.
Da sauri Ishmah tace.
“Eh Laylah shiryata”.
Jin haka ne yasa Laylah jan hannun Afisha sukayi ɗakinsu.

Addawa kuwa da sauri fara jujjuya kai tare da sharce hawayene daya ciko mata ido kana tace.
“A'a Ishmah kada akai Afisha.
Ki bashi haƙuri.
Kada kiyi wannan gaggawan Tajj bazai lamunci hakanba”.
Cikin tarin mamaki da tsoro Ishmah ta zazzaro idanunta tare da cewa.
“Haba dai Addawa iyayensa nefa mahaifinsa nefa, ya isa yace kada yaransa suje inda iyayensa suke”.
Cikin sauri Addawa tace.
“Tabbas kuwa, wallahi bazai taɓa barin yayansa ko wani nashi yaje wurin Malam Muhammad ba, kuma kema in kikayi wannan ganganci inada yaƙinin zaki fuskanci tashin hankali da baki taɓa fuskataba a tare dashi.
Dan haka kada Afisha taje.”
Ido Hamisu ya zuba musu Ayeed da Ayaan kuwa kama hannun Ishmah sukeyi suna cewa suma zasuje.
Ita kuwa Ishmah cikin son shawo kan Addawa tace.
“Please dan Allah Addawa kada muyi haka dake, dan Allah ki daina cewa kada Afisha taje, ki bani goyon baya taje”.
Da sauri tace.
“To ko kira Tajju ki gaya mishi in ya amince taje sai suje”.
Cikin zare ido Ishmah tace.
“A'a wlh bazan kirashi ba, Addawa ke da kanki fa kika rantse min yanzun nan bada jimawa ba, kikace bazai yarda ba, ta ya zan kirashi, ni dai lamuncewarki nake nema, ai bani zan jeba Hamisu ne zai kaita”.
Cikin tsoro da fargaba da rashin son abin Addawa tace.
“In yazo ya sani fa”.
Da sauri Ishmah tace.
“Ai bazama ya sani ba”.
Kai Addawa ta jujjuya tare da cewa.
“Ni dai Ruƙayya ba bakina ba hannuna a cikin maganar nan kuma duk abinda zai je ya dawo kada ki sani a ciki.
Kuma zan kuma jaddada wa Ishmah kada ki bari Afisha ta je”.
Riƙo hannun Addawa ta kuma yi da kyau tare da marairaice fuska tace.
“Naji na yarda komai ya faru ba ruwanki a kaina wakai dai ni alfarma da zan nema kada ki gaya mishi in ya dawo kin san su Afisha duk in na kwaɓesu bazasu gaya mishi ba, har sai a hankali zan mishi bayani”.
Cikin fushi Addawa ta janye hannunta tare da cewa.
“Bazan faɗa ba, Amman kuma ba yawuna a tafiyar Afishan”.
Tana kaiwa nan ta koma ta zauna kan kujerar bayanta, tare da fara tunono sharaɗin Yah Abana,

da kuma hasashen irin abinda zai faru in Tajj ya dawo ya samu wannan labarin.
Cikin sanyi Hamisu yace.
“....

Alamomin infection sune kamar haka. Rashin sha'awa. Ƙaiƙayin gaba Kiji idan ya fara miki ƙaiƙayi kamar zakiyi hauka. Warin ko ƙarnin wurin. Fitar farin Ruwa mai fatsi-fatsi. Ƙurajen su ɗan fetso ƙananan ko ƴan manya, melewar fatar wurin, Tusan gaba. Bushewar gaba, Rashin ni'ima. Buɗewar gaba, domin har budurwa infection na iya buɗata. Ciwon mara ko ciki mai tsanani yayi al'ada, rashin haihuwa, domin har baƙin mahaifa take toshewa. Ko kirinƙajin wani abu na miki yawo ƙasan mara, ko jin zafi yayin yin fitsari, da kuma sdw, da dai sauran abubudann ban  lissafa Sune manyan alamomin infection.

Shin kin kuwa san illar da infection keyi miki, amman kinajin ɗaya daga cikin alamominta kinyi bulum buƙui da ita a jikinki. To bari kiji illolin infection wato cutar sanyi.
Rashin haihuwa, ƙyara da hantara a wurin miji domin muddin kina tare da ita baki da wata daraja a idanu nai, sabida ƙyamas kike ba damshi bare wata ni'ima mai Taste, Kinga kenan shinfida ta lalace, in kuwa shinfiɗa ta lalace dole kiga sauyin fuska, domin su maza dole sunason wurin da kwaranya, zaki kasance baki da wani daɗi da ɗumin da mai gida ke buƙata. Kinga duk tsabtarki da kyanki da iya girkinki shinfidarki ta zama lami. Kiyiwa Allah ki nemawa kanki lafiya ki samawa mijinki da ke kanki nitsuwa.

KADA KUJI IYA WANNAN DOMIN AKWAI MUGUN INFECTION WANDA BAYA BAYYANA KANSA. Wanda kawai sai dai kijiki, kamar kwalta kin bushe ƙyamas ya dauke miki dukkan sinadaran ni'imomin ki, da sha'awarki, duk kayan matan da zakisha a wofi zadai kiji ƴan uwa da abokan arziki da ƙawayenki na yaba miki magunguna GARKUWAR MA'AURATA, amman ke in kinsha jiya I yau,  duk nacin oga da yi miki wasannin bazaki ji sha'awa ba, toh wlh muguwar infection ce, wacce bata bayyana kanta har sai ta gama yi miki rugu-rugu. Ta lalata miki zaman aure. Lokacin da zata bayyana sai kiji Doctor's suna kira miki, ovarian cyst, ko kuma fibrod duk a cikin chronic infection ne yar uwa.

INFECTION set ɗinmu na kowa da kowane Mata, Maza, Bazawara, Budurwa, Maijego, Yara, Ke yar uwa Wlh har maiciki zatasha, bashi da matsalar komai Maganin na Gargajiya ne mai rakake INFECTION ya fito miki dashi, wlh duk nacin infection koda na cikin mahaifane bi'izinillahi ta'ala zaki rabu dashi, cutar infection cutace mai masifar naci, so yar uwa kana dole ki nace masa da maganin set ɗin na 10k ne kuma maganin kala biyarne nasha da kala uku na tsarki ɗaya na shafawa ɗaya. Yar uwa idan har kin saya to kiyi ƙoƙarin kisha da mijinki, in akwai abokiyar zama, kisa miji ya saya mata, domin ko kin rabu da shin dai ita tana dashi tofa kin kashe macijine baki cire kaiba, ma'ana zai sake dawo miki,

idan kuna da yara suma a saya musu, domin tsoron kada ya riƙa a jikinsu musamman ya'ya

mata ya buɗa miki ƴa tun tana ƙaramarta, ki aurar da ita miji na muku kallon lalatattun iyaye da baku iya bada tarbiyaba. Saboda yamayin garin yasa ina raba rabin set ɗin in sa miki komai rabi-rabi 5k amman na ɗan saki Garabasar 4k set ɗin 10k ne Amman yau 8k ne. Idan kin san a shirye kike ga account number na nan 0005388578 Jaiz bank AISHA ALIYU GARKUWA, ki turo kuɗinki kafin kiyi min mgn ta WHATSAPP NUMBER'N na 08069423567 sai ki turo min shaidar biyanki, domin akwaishi Available ko yau kika tura kuɗinki, gobe kayanki zai taho, ina bada sari ko sayan ɗaɗɗaya. Farashin Sari da sauƙi daga kan mutum 3 ko 6 ko 12. Kai ko na mutum 24 kikeso in Sha Allah zaki samu ina kuma bada sarinsa a farashi mai sauƙi.
Please dan Allah in dai kinsan baki shirya sayaba kada kimin mgn ki bari sai kin shirya. Taku ce dai GARKUWAR MA'AURATA

Dan Allah in dai kinsan baki shirya sayaba kada kimin mgn, masu cewa wai sun goda suga number'n nayine, ko kuma a'a bari dai in na shirya zan sake miki mgn, ko kuma yanzu dai kuɗin bai cikaba tukun sai sun cika, ko kuma a wanne gari kike, kai munyi nisa, toh ai duk nisan state da kike ba ruwan mota ba inda bazai kai mikiba, nake turawa ƴan ƙasashen wajema. Kuyiwa Allah da Manzonsa in dai in kinsan Baki shirya sayan kaya ba kuyi haƙuri kada kumin mgnar ku bari sai kun shirya,kada kuzo mu ɓatawa juna lokaci Allah y sani na tsani bana son mutum yaga na mishi ba dai-dai ba nima Kuma bana so ayi min wasa da hankali a harkar kasuwanci 🙈🤗🤣, duk bayani na gamayi in dai saya zakiyi ga kuɗin kaya ga account no ga numberta ai sai ki biya kawai kafin kimin mgn. Tunda dai ga alamominshi duka.

By
*GARKUWAR MARUBUTA**INDA RAI*
Part 3 page 3
Na
*Aysha Aliyu Garkuwa*

*Mutanen Niger gafa dama ta samu, na sauƙin Delivery Nigeria to Niger, ina tura kaya a garuruwan nan cikin aminci da yardar Allah. Nyemay, Maraɗi, Tawa, Arlit, Zinder, Agadaz, Madawa. Da duk sauran garuruwan dan yardar Allah, sai dai ɗan tsadar kuɗin mota, wanda hakanne kuma yasa nake sake muku special bononza na kayana na Ɗa'a da Maganin Infection da kuma kayyakin ƙamshi turatukan wuta da kulacca da su Humra da dai sauransu. Ina muku araha don samun sauƙi. Inada yaƙinin in sha Allah zakuji daɗin hakan.*
Akwai haɗin amarya budurwa mai ƙarancin shekaru da mai matsakaicin shekaru da kuma mai ɗan yawan shekaru, kana haɗin amarya bazawarar da take da ragowar ƙuruciya, da mai matsakaicin shekaru da wacce shekaru sun ɗan ja, hadi dai-dai da halittarki ƴar uwata, ƙawata, ƙanwata, ƴata, ƴaƴata, kai harma da ke kakata, akwaisu masu maida tsohuwa yarinya, duk mutuwa da sakewar fatar nan zata tattare da tsuke ta katse ta rayu da ni'imtaccen yayyafin gyaran zaman aure.
To wai ke mai jego ina kike akwaisu fa naku haɗin, in ma yawan haihuwa yasa wurin ya sake ya kuma ƙafe, barden goyo ko ɗanyen goyo, akwai haɗinku.

Zaki min bayanin me matsalarki!
Sakewa ne? Rashin ni'ima ne? Rashin feeling ne, ko rashin kuzari ne.
Duk fa akwai haɗinshi.
Kun dai san farashin kayana step by step ne, bana barin Customer tazo da kuɗin duk ƙanƙantatsa ta juya ba kaya, shiyasa mazubin kayana ke cikin manya da ƙananan robobin da manya. Manya set ɗina daga 50k ne 60k 70k 80k 90k sai sha kunɗum uban aikin 100k sai kuma ƙananan set ɗina da suka fara daga 40k zuwa ƙasa 35k 30k 25k 20k 15k sai kuma ɗan Autan haɗina 10k banayin haɗin ƙasa da 10k sai kwanan Ƙasaitacciyar mace 5k. Sai kuma set ɗin maganin Infection set 10k half set 5k Amman daga jiya zuwa yau ina Bononza set 8k half set 4k ne.
Akwai kuma turatukan wuta da kulacca da su Humra kala-kala da ban da ban, suma haka ne farashin su. Yake suma ina araha ina hana bashi ina kuma yin asusu wa Customers na. Idan kina buƙatar ga Account no na nan 0005388578 Jaiz bank Aisha Aliyu Garkuwa, sai ki turo min shaidar biyanki ta wannan number 08069423567.

“Adda To in Yah Afif ya dawofa kafin mu dawo”.
Cikin sanyi tace.
“Shida sai gobe zai ɗauko parsingers ɗin Jordan, in ya diresu ne zai kwaso na Qatar a Jordan ɗin, ta zai dawo yau”.
Kai Hamisu ya jinjina tare da cewa.
“Toh Amman kinaga ba matsala”.
Da sauri tace.
“In sha Allah kuwa”.
Dai-dai lokacin Laylah da Afisha suka fito daga ɗakin nasu.
Wani irin ƙelli da ƙamshi Afisha yake zubawa. Egypt Abayace Blue black mai masifar sulɓi yasha Diamond stones da suke baza ƙyalli.
Tayi mata Rollin kanta da gyalan rigar, tayi mata wannan shigar nen kasan cewar yau jumma'a dan suna da al'adar sa sutura ta musamman duk ranar jumma'a.
Sosai tayi kyau kamanninta dasu Hamida ya fito fili musamman Rashida.
Cikin zumuɗi tace.
“Ammeey na mun tafi”.
Sunkuyowa Ishmah tayi tare da sumbatar goshinta cikin rashin jin tsoron me zai je ya dawo tace.
“Allah ya kaiku Ify Mamana ki gaida min ya abana.”
Sai kuma ta kalli Ayeed da Ayaan da sukayi gaba.
Muryar Addawa da tajine yasata kamo Ayeed da Ayaan ɗin.
“Hmmm ni dai nawa ido wato bayan Afisha harda su Ayeed ɗin zaki tura?”.
Da sauri ta ruggume yaran tare da cewa.
“Kuyi haƙuri anjima da dare zamuje tare.
Kunga yau jumma'a kada ki rasa jam'i ku bari Zulaihat tazo ta shiryaku”.
Sai kuma ta kalli Laylah da ke cewa.
“Ayyah Ammeey nima zanje”.

Kai ta gyaɗa mata alamun taje".
Ita kuwa Addawa cikin jin takaicin rashin bin umarninta karo na farko da Ishmah tayi a tsawon zamansu ta zamansu ta miƙe ta koma ɗakinta.
Ita kuma Ishmah kitchen ta koma tare da danƙawa Zulaihat hannunsu Ayeed tana faɗin.
Je ki musu shirin jumma'a Kinga har lokacin ya ƙarato.

Ethiopia.
Cikin mamaki Mom Amal ke kallon Meymey da ke zaune a gabanta yayinda gidan ke cike fal kamar yadda suka saba duk ranar jumma'a.
Murya a disashe ta gaida Hajia Babba kana Ummu Aryan.
Sai kuma ta kalli Mom Amal cikin tsananin dana saninta a duniya tayi kwaffa tare da gaida a sukane,  kana ta kalli Ummu Aryan tare da cewa.
"Yah Abana fa?".
Ta ƙare mgnar cikin mabayyanin damuwa da nadama.
Da sauri Mom Amal tace.
"Baya nan yayi tafiya".
Cikin sauri tace.
"Ina yaje?".
Cikin takaici da baƙin kishi da safin rasa gane inda lamuran Yah Abana ya dosa tace.
"Muma duk ba wacce tasan inda yaje, ni ban ma san yau zaiyi tafiyar ba".
Murmushi Hajia Babba tayi tare da miƙewa tsaye kana tace.
"Kai wallahi ke ma dai Mom Amal kamar baki san malam ba to ina zaije daya wuce umrah."
Hararan ƙasa-ƙasa tayiwa Hajia Babba tare da cewa.
"Da alamu kuma kece baki karanci lamarin malam ba."
Cikin sanyi zazzafin kuka Meymey tace.
"Ummey fa".
Ummu Aryan na bin bayan Hajia Babba tace.
"Tare suka tafi ai Meymey, Amman su Halima da Zakeeya nan ki isa mana".
Daga nan suka fice.

Suna fita Kabiru da Aryan suka matso kusa da Mom Amal ɗin.
Ita kuwa Meymey yunƙura tayi da biyar miƙewa sai kuma ta koma ta zauna saboda jin wasu kalamai da Aryan yakeyi dole ta koma ta zauna cikin yanayin da ita kanta bata taɓa zato ko tsammanin zata yishi ba.
Tana zama Amal na shigowa.
Gyara zamanta tayi tare da fuskantarsu da kyau gami da gyara riƙon wayarta nan sukaci gaba da tattaunawa.

Sai kusan bayan awa biyu kana Aryan da kanshi ya maida ita, dan sun samu mafita a zaman nasu.

Cikin lumshe ido Ishmah ta kalli Laylah dake cewa

“Ammey nayi mamakin ganin harda Ummey fa Yah Abana yazo.”
Sai kuma ta kalli Addawa da begen yarta yasata cewa.
“Da nasan harda Fatima na akazo wallahi da dani zaku tafi, kuma da munje tare da baza'a bar Afisha a canba”.
Murmushi Ishmah tayi tare da ɗan lumshe idanta dan jin zuciyarta na tsinkewa tare da faɗuwa ras-ras sai kuma ta danne abin da addu'a tare da cewa.
Ai Hamisu yace Yah Abanan yace gobe da sassafe yaje ya ɗaukota.
Cikin jin fargaba Addawa tace.
“Kwana ma zatayi kenan”.
Da sauri Laylah tace.
“Hmmm Addawa kenan saifa kinga yadda Yah Abana da Ummey suka haɗe wuri ɗaya suka ruggume Afisha Ummey fa harda hawayenta ta rinƙa cewa dan Allah mu bar musu Afisha ta kwana, nima fa da kyar ta sakeni.
Tana ta mamaki wai na girma.
Ammey wai yanzu nafi da kyau?”.
Ta ƙare mgnar cikin sigar tambaya da jin tasowar shaƙuwa da son Ummey da ahlinta na Ethiopia baki ɗaya.
Cikin murmushi Ishmah ta jawo hannun Daddey tare da cewa.
“Sosai ma kuwa Laylah ai ƙanina ya tsinci dami a kala.
Yanzu muje muyi salla sai kizo mu shiga kitchen zanyiwa su Yah Abana abinci da magrib ku kai musu ko”.
Sai kuma ta kalli Addawa tare da cewa.
“Addawa me Ummeey tafi so a abinci”.
Cikin ɗan jin sassaucin haushi. Ishmah tunda akace mata da yarta akazo tace.
“Daga ita har malam suna son samun fura da nono mai kyau sai kuma Couscous shine abinda sukafi so”.
Cikin sauri tace.
“An gama, muyi sallah ko Laylah mu shiga kitchen kafin waɗannan su dawo daga sallan jumma'a”.

Gab da Magrib ya shigo gidan, cike da nishaɗi da farin cikin samun dawowa a yau a madadin sai gobe sai wani irin Ni'imataccen ƙamshin mai ɗan ƙaren daɗin shaƙa yake zubawa. Sajen san nan yayi lip-lip gwanin ban sha'awa sai ƙyalli da sheƙi yake zubawa.
Da ka ganshi ka ga alamun gaji tattare dashi.
Fuskarsa ɗauke da yelwataccen murmushi ya tura ƙofar corridor tare da sallama a binsa sai kuma ya ɗan buɗe murya da ɗan ƙarfi yana faɗin.
“Hello my happiness Ummey na, ga Abeey ya dawo.
My Twins Ina kuke ga Abeey.
Daddey Sweet heart Abeey na kira”.
Ya Salam.
Shine abinda Addawa ta furta da ƙarfi tare da firgici.
Ayeed da Ayaan kuwa da suke ɗakinsu a guje suka fito bisa dukkan alamu alwalan sallan

magrib sukayi.

Ishmah kuwa da sauri ta ɗan juyo tare da fitowa daga kitchen ɗin dan jin kamar muryar mijinta na cewa.
“Hello babey ina kike”.
Sai kuma ta tsaya kamar an dasata saboda ganin yess shi ɗin ne dai.
Shi kuwa Tajj da sauri ya ɗan rage tsawonsa tare da buɗewa su Ayeed hannunsa, ai kuwa a guje suka abka jikinsa.
Sai kuma ya fara jujjuya kanshi tare da cewa.
“Ummey na ina kike, Afisha am back”.
Sai kuma ya saki Tattausan murmushi ganin Daddey dake bacci gefen Addawa jin muryarsa ya tasheta ta miƙe da sauri tana wangale baki tare da nufishi tana ɗan tangaɗin bacci.
Shafa kansu Ayeed da Ayaan yayi tare da sumbatar gishi gami da sa musu al'barka, sai kuma yayi sauri rungumar Daddey data faɗa jikinsa tare da miƙewa tsaye yana nufo gaban Addawa da tayi kamar tsoratacciya.

Ganinshi gabanta ne ya sata miƙewa dan sanin in dai yayi tafiya ya dawo sai ya ruggumeta ita da matarsa da yaransa da Hamisu.
 Laylah da Zulaihat kuma ya shafa kansu yasa musu al'barka.
Rugumetan yayi irin yar rungumar gefen nan sai kuma ya ɗan kalleta cikin tsananin sonta yace.
“Kina Ifya?”.
Yayi tambayar yana waige-waige.
Cikin aro ƙarfin halin um toma ita ina ruwanta taga Ishmah ma bata wani ruɗeba.
“Lfy Lau Alhamdulillah ya hanya, kai da muke tsammanin ka jiya sai kuma mu ganka yau”.
Yana shafa kan Laylah da ta iso gabansa yace.
“Eh an samu parsingers ɗin Qatar ne da yawa a Malli shiyasa kawai aka bani su”.
Sai kuma ya kalli Laylah tare da cewa.
“Allah ya miki al'barka ina,  little Ummey?”.
Da sauri duk suka juyo suka kalli Ishmah jin tayi wani irin gyaran murya tare da matsowa kusa dashi tana faɗin.
“Ni da ba'a damu da niba ko sau ɗaya ba'a nemeni ba”.
Da sauri yasa hannunsa ya kamo nata tare da jawota jikinsa ya ruggumeta cikin so da alamun begen ta a ɗan kwana biyu da yayi baya nan ɗin yace.
“Ai ke heart beat nace, ko ban tambayeki ba muna tare, ina jin motsinki a jikin dukkan bugun zuciyata Ina Afisha”.

Cikin ɗan shayi kaɗan tace.
“Taje gidan Rahma ne”.
Fuskarsa ya ɗan sauya sai kuma ya ɗan jujjuya kai.
Tare da ruggume Hamisu kana ya sawa Zulaihat al'barka.
Cikin ɗan gajeren tsaki yaja tare da cewa.
“Me yasa baki gaya minba ta tafi?”.
Yess ta sani duk inda yaransa zasuje dole sai an gaya mai ko baya nan koda ko gidan Rahman

ne da Dr Abbas.
Ya ƙare tambayar ne kuma da tsareta da ido.
Cikin sanyi tace.
“Afwan nayi laifi amman kayi haƙuri bazan ƙaraba".
Kai ya sunkuyar tare da kallon agogon hannunsa.
“Lokacin salla yayi mu tafi masallaci.

Daga nan suka fice.

Ita kuwa Ishmah jan hannun Laylah tayi tare da cewa.
“Karfa ki yadda ku gaya mishi inda Afisha take zan gaya mishi a hankali.
In munyi salla ki ɗauki basket ɗin abin sun Yan Abana kisa a mota.
Suna dawo masallacin zan jashi sama, sai kuje ku kai musu abinci, ku ɗauko Afishan dan kinsan baya barinku kwana a wani wurin.
Kai Laylah ta gyaɗa kana ita da Zulaihat suka ɗauko womars ɗin abincin daransu suka shirya a kan dinning table.
Addawa kuwa cikin kallon Baga irinta nan ba, ni dai ba ruwana ta wuce tayi ɗakinta.
Itama Ishmah ɗakinta ta shiga.
Bathroom ta wuce wanka ta fesa tare da yin brush kana tayi alwalar.

Tana fitowa ta shafa mai tare da murza kulaccar sirri da shu'uman hummara a jikinta.
Wasu Tattausan riga da wondo masu masifar sulɓi tasa, royal blue color sai sai kuma ta ɗaura after dress akai fari ƙal.
Hijabi ta zura kana ta kabbarta sallah.

Basu fito masallacin ba sai bayan an idar da isha.

A hankali suke tafiya yana riƙe da hannun Ayeed a gefen damansa Ayaan a gefen hagu Hamisu na daga fensa ta gaba kaɗan.
Cikin nutsuwa ya kalli Hamisu dai-dai lokacin da suka iso bakin ƙofar shiga cikin main parlor nasu.
Ɗan murɗa handile ɗin yayi kana ya tura ƙofar tare da cewa.
“Yauwa kai Hamisu wuce gidan Dr Amdaz ka ɗauko min Afisha”.
Cikin sauri Ayeed yace.
“Abeey ai Adda Afi na wurin Yah Abana, mu Ammey ta hanamu zuwa”.
Rashin gargaɗin da Ishmah ta sha'afa batayi musuba yasa Ayeed wannan maganar.
Cikin rashin fahimtar mgnar da kyau yace.
“Kai Ayeed wuran ya Abana kuma, ai gidan Aunty Rahma taje.”
Da sauri Ayaan yace.
“A'a Abeey wurin Yah Abana Uncle Hamisu ya kaita, yakira sunyi waya da Ammeyn mu”.
Cikin rashin gamsuwa da fahimta ya juyo kan Hamisu dai-dai lokacin kuma Hamisu ya kai hannunsa ya ɗan bugi bakin Ayaan alamun yayi shiru.
Cikin sauyawar fuska in one time ya tsare Hamisu da ido tare da cewa.

“Kai Hamisu ina Afisha take?”.
Kai Hamisu ya ɗan sosa tare da cewa.
“Ah, ummm, ehh, to nima ɗazu na dawo ban san”.
Cikin sauri Hamisu yayi ƙasa da kansa dan jin wani irin hautsinennen tsawa daya daka mishi.
“Kar ka kuskura ka yarda ka fara yi min ƙarya, ina ka kai Afisha?”.
Cikin tsoronsa da girmamawa yace.
“Eh can take”.

Cikin wani irin tashin hankalin da yasa lokaci ɗaya idanunsa suka firgito waje, tare da fara sauya launi daga fari zuwa ja ja ja.
Tuni murmushin fuskarsa ya ɓace sake hannun su Ayaan yayi tare da kusa kai cikin farko yana sunawa Ishmah kira da sunan da rasan in ya kirata ba wasa ko wani shauƙin so iya zallar gsky da matsayinsa a mijinta yake nunawa.
“Aysha! Aysha!! Aysha!!!”.
Ya kira na ukun da ƙarfi tare da nufar ɗakinta, a bakin ƙofar sukayi kiciɓis.

Addawa kuwa jin kiran ne yasata fitowa Laylah da Zulaihat dake zaune a falon kuma miƙewa tsaye sukayi saboda ganin yadda yake a fujajan.
Idonshi ya tsaida cikin nata murya cike da matsayin miji kuma uba ga yayansa yace.
"Aysha ina Afisha”.
Cikin aro jarumta tace.
“Nace maka tana gidan Ra.”
Da sauri ta rumtse idanunta cikin tsanani rawan jiki saboda bahaguwar tsawar daya danna mata wacce ta nemi kuramta mata kunnuwa.
“Kada ki zubda ta hanyar yin ƙarya ina kika tura min ƴata?”.
Cikin tattaro ragowar jarumtarta da ƙarfin guiwarta tace.
“Tana wurin Yah Aban...”.

Da sauri tayi ƙasa da kanta tare da toshe kunnenta jiyo muryar shi na amsa kuwa cikin tsananin tsawa da fushi da fusatar da tasa gaba ɗaya jikinsa rawa yace.
“Da izinin waye kika kaita? Addawa ya za'ayi ki bari s kai Afisha wurinsa”.
Cikin sauri Addawa tace.
“Wallahi nayi iya yina Amman Ishmah taƙi saurarona, Ni bada izinina ko da yardata ta turata ba, na hanata ma taƙi hanuwa dole na zuba mata ido”.
Cikin rawan jiki murya a hargitse lissafinsa na ƙara barin kansa in ya tuna shike nan yau yarsa ta zama sanadin mutuwar auren iyayensa, shike nan tsinuwar Yah Abana ta hau kanshi, shi kenan daga yanzu zai fara rayuwa da Allah ya isar mahafinshi wanda ya sani kiyaye sharaɗinsa ne yasa baiga maaifa a rayuwarsaba,tunda dama yace in ya sake ganinsa ne ko alaƙanta kansa da ɗansa ko yin alaga da yayansa ne sharaɗin tsinuwar da Allah ya isan garma da sakin Ummeynsa murya a hautsine yace.
“Aysha kin cuceni kin tozarta min darajar auren mahaifiyata kin sani a hufushin iyayena nace ma da izinin waye kika tura min ƴata can ke kika haifa min itane ko ke kika halitta min ita ko kece kika bani ita da zaki yanke hukunci a kanta har Addawa ta hanaki ku ƙi hanuwa”.

Cikin son tunasar dashi tace.
“Naga ai iyayenka ne, ya kamata ka tuna darajarsu tunda ai kaima mallakinsu ne bare yar da ka haifa dan Allah ni ka daina min irin wannan ihun a kaina...”
Cikin rufewar ido alamun ya fara kasa control ɗin zuciyarsa da jikinsa dan illahirin jikinsa karkarwa hakeyi tuni fuskarsa tayi jazur idanunsa kuma kamar zai zarosu waje cikin tsananin hargitsewar tunani ya danna mata tsawa cikin umarni yace.
“Maza ki wuce kije ki ɗauko min ƴata.”
Cikin zuba mishi ido tace.
“Wallahi ba inda zanje bazan ɗaukotaba, sai dai kayi duk abinda kake son yi”.
Cikin wani irin rawan jiki da kiɗima da hauhawar fushi.
Ya ɗaga hannunsa da ƙarfi ya yarfa mata wasu irin tagwayen maruka harda gambonsu.
Kau! Kau!! Tas!!! Marukan da suka sa jinta ya ɗauke cak sai dummmm kunuwanta ke bada wani sauti.
Ganinta yayi ɗib sai wasu taurarin take gani suna gilmawa ganinta.

Da sauri Addawa ta riƙo hannunsa ganin ya sake ɗago hannunsa zai yarfa mata wani marin.

Hamisu kuwa cikin sauri yaja hannun Ayeed da Ayaan ya juya dasu ɗakinsu ba tare da sun ƙarasa shigowa ba.

Laylah kam tuntuni ta bar falon da gudu ta nufin ɗakin Addawa hakama Zulaihat ta mara mata baya.

“Yah Salam Tajjudden ka rinƙa maimaita innalillahi wa innalillahi rajiun, zakaji sanyi a ranka”.
Jin yadda jikinsa ke rawane yasa ta fara jan hannunsa.
Ita kuwa Ishmah wani irin maraitacccen kuka mai cike da tarin takaici da shaiɗan ke kitsima mata ta juya ta koma cikin ɗakinta.
Shi kuwa Tajj da ƙarfi ya fara kiran Hamisu a tsawace.
Da sassarfa Hamisun ya iso inda yake.
Cikin bada umurnin yace.
“Muje ka kaini inda ka kaimin yata”.
Cikin sauri Hamisu yace.
“Toh”.
Tare da juyawa ya nufi waje.
Cikin fusatar yabi bayan Hamisu, kusan a tare suka shiga Mota kana Hamisu yaja moto suka tafi.

Dubai ƙarfe takwas dai-dai ta samu su Adaya a wurin tantance lafiyar yaran da zasu gudanar da gasar rawar ta ko wacce ƙasa.

Cikin farin ciki su Adaya suka fito dan an gama duba tawagar Ethiopia.

“Gsky Adaya na gaji yanzu dai mu koma gida, tun ƙarfe tara na safe fa, muka iso Dubai muketa yawo kamar zomawaye ni bacci nakeji”.
Cikin sauri
Izzin yace.
“Yesss yanzu dai kam ya kamata mu koma ma sauƙinmu dan mu samu isasshen bacci saboda mu samu mu tashi da wurin mu samu hallatar wurin gasar da wurin tunda ance ƙarfe takwas dai-dai na safe za'a fara”.
Cikin gamsuwa da maharsu Adaya ta gyara jinginar Yasir a jikinta kana tace.
“To ba laifi mu koma”.
Ta ƙare mgnar tana kallon yan sauran tawagar tasu.

Ethiopia.
Mommyn Meymey ta ɗan Lumshe idonta tare da kallon Abban cike da damuwar abinda ɗiyarsa ta aikata cikin sanyi tace.
“Itama taje bata sameshi ba, wai sun tafi Umrah da Ummeyn Affi wlh da suna ƙasarnan a yau a daren nan zanje in basu haƙuri in wanke kaina”.
Cikin rasa abin cewa ya zuba mata ido.

Ita kuwa Meymey kwance take a ɗakinta waya takeyi da Yah Aryan yana ƙara yi mata ƙarin bayani kan plan C ɗin dan sun A an koreshi sunyi B an barranta dashi sauran C kuma rabashi da duk farin ciki da daraja a duniya.

Qatar
 Afisha ce zaune a tsakiyar falon bisa Tattausan turkey carpet ɗin dake wurin bisa dukkan alamu yanzu suka dawo daga shopping mall.
Dan ta zuba abubuwan wasane a gabanta kama daga su manya-manyan Teddi sai kuma yan madaidaitan baby masu kyau da aiki da batir, ga samon system da tafi farin ciki a kansa, sai lodin suturu sun kai kala bakwai su chocolates sweets.
Ga kuma set ɗin kayan kitchen na wasan yara kama daga tukwane kofuna plate sai kuma wani ɗan kekkyawan carbi dake hannunta.
Ɗaya daga cikin kayayyakin bacci da suka saya mata ne a jikinta riga da wondo pink color masu ɗan kare taushi da ƙyalli sai zanen heart fari da ja a jere a jere  , sunyi cib cib da ɗan jikinta, yayinda Ummey ta tubke mata gashinta gida uku ɗaya a ƙeya ɗaya a gefen dama ɗaya a gefen hagu sai kuma ta ɗan saka mata head band ja.

Wani irin murmushin dake bayyana tsananin jin daɗinta da farin cikin zama a tsakiyarsune bisa fuskarta da sauri ta miƙe tsaye tare da ɗago wata riga da siket farare da zanen blue, kanta Yah Abana ya shafa cikin tsananin so da ƙaunarta yace.
“Ya akayi”.
Sai kuma ya sumbaci goshinta da sauri ta hau bisa kujerar tare da sumbatar kumatunsa.
“Abban Abeey na ina sonka”.
Kanta ya kuma shafawa tare da cewa.

“Ni nima ina sonki”.
Cikin sauri ta kuma sumbaci Ummey a kumatu tare da cewa.
“Ummeyn Abeey kema ina sonki, sosai fa dan Abeey na yace min duk duniya kinfi kowa sonshi shiyasa yasa min sunanki kuma fa Abeey yafi sona fiye da kowa a duniya”.
Da sauri Yah Abana ya ɗan ture ƙeyarta tare da cewa.
“Ƙarya yake miki nafishi sonki”.
Ido ta zazzaro tare da cewa.
“Hyyyyh Yah Abana Kayi Astagfirillah, Abeey na baya ƙarya bakin dake karanta Kur'ani ai bazaiyi ƙarya ba”.
Yadda tayi mgnar ne da zare idon yayi matuƙar basu dariya.
Dai lokacin kuma suka ji ana ƙwanƙwasa musu ƙofar.
Da ido Yah Abana ya nunawa Ummey alamun taje ta buɗe.
Dan tayi zaton mai Delivery ne ya kawo saƙon Kur'ani da sallaya da suka saya Afishan.

Cikin nutsuwa da danne bugun zuciyata ta buɗe ƙofar tare da janta baya ya zama tana bayan ƙofar ya ɗan ɓoyeta.

Shi kuwa Yah Abana dake fuskantar ƙofar ɗakin cikin wani irin yanayin da bazai taɓa iya misaltashi ba, ya miƙe zaune daga kishinƙiɗar da yayi.

Shi kuwa Tajj daya kutso kansa cikin ɗakin.
Wani irin raunin zuciya da jikine sukayi mishi dirar mikiya  wanda yasa shi fara ɗaga saeunshi a hankali yana ƙara shiga ciki.
Ita kuwa Afishan da ta bawa ƙofar shiga baya tana miƙawa Yah Abana wata kekkyawar baby tana cewa.
“Ya gamin ledarta ita wannan takwarar Aunty Laylay ce na mijin kuma Uncle Hamisu zan yiwa takwara”.
Ganin duk maganar da take yi bai kulata bane, yasa tayi saurin juyowa dan son ganin me yake gani.

Ita kuwa Ummey yana wuceta taji ƙamshin jikin ɗanta da hancinta bazai iya mancewaba.
Wani irin mutuwar jiki da raunin zuciyane suka haɗu suka tsinko mata ruwan hawayen idanunta, hakan yasa ta fara binshi a baya a hankali a hankali saboda duk kuzarinta ya bar jikinta tuni hawayen ta ke zirya har suna gangarowa kan ƙirjinta.

Ita kuwa Afishan ganin Abeeyn tane yasa tayi wani irin tsalle da ihun farin ciki tare da rugowa a guje ta nufi inda yake.
“Oyoyo Abeey Yah Abana Ummey ga Abeeyna”.
Cikin sauri ya durƙusa kan guiwowinsa kamar yadda yake musu a koda yaushe hannunsa ya buɗe mata.
Rungumeta yayi tsam a jikinsa tare da rumtse idanunsa.

Shi kuwa Yah Abana ƙasa yayi da kansa yana sauraron bugun zuciyarsa.

Ita kuwa Ummey kujerar dake gab kusa dashi ta zame dirsham ta faɗi zaune a kai.

“My happiness meyasa zaki tafi wani wurin baki gaya minba. Afisha gidan ba daɗi da na dawo ban sameki ba”.
ƙara  lafewa tayi a jikinsa tare da cewa.
“Abeey ban san yau zaka dawo ba, da nabi su Uncle Hamisu na koma, kayi haƙuri kar kayi fushi dani Yah Abeey”.
A hankali ya ɗan janye ta daga jikinsa, tare da ɗan sumbatar goshinta sai kuma ya riƙe kafaɗunta da hannayensu duka biyu murmushin da yasa hawayensa zubowa ya sakar mata cikin sauri ya kamo lip inshi na ƙasa ya tauna da ƙarfi wan ko zai samu hawayen raunin nasa su tsaya Amman ina sai ma ƙara kwaranya da sukeyi.
Kanshi ya sunkuyar tare da tsurawa yatsun sawun Ummeynshi ido.
Shekara tara kenan bai sa iyayensa a kwayar idanunsa ba, yana raye suna raye bai mutuba basu mutuba sai sharrin magauta da nakircin makirai da fushi da zuciyar riƙo da rashin yafiyar mahaifinsa ne duk suka jaza mishi.

Hamisu kuwa a hankali ya raɓe bakin ƙofar tare da maida ƙofar ya rufe.

Ita kuwa Afishan ganin mahaifinta na zubda hawayene yasa nata idon ciccikowa tib da wahaye yan hannauenta ta ɗaura kan kuncinsa tana sharce mishi ruwan hawayen tare da fara magana cikin raman muryar kuka.
“Abeey kayi haƙuri bazan sake tafiya wani wuri ban gaya maka ba, kayi haƙuri ka daina kuka. kada kayi fushi dani Abeey”.
Cikin raunatacciyar Muryar da take wani irin sanyi da rawa ya buɗe baki a hankali tare da fara fito da maganar daga cikin ƙahon zuciyarsa.
“Afisha na banyi fushi da keba! Kuma in sha Allah.
bazan taɓa yin fushi da keba har illa masha Allah.
Duk girman laifin da zakiyi min bazan yi fushi da keba, sai na fara bincike akan haƙiƙanin shin kinma aikata laifin ne, koko ƙazafine ko sharrin magauta”.
Ya dire mgnar cikin tsananin raunin murya na rawa hawaye na tsiyaya, yana maganar ne tafe da hannunka maisanda da cikekkiyar falsafa da har ga Allah shi bai ma san yana yinsuba.

“Uhhhhyyyyym”. Yah Abana ya fesar da wani irin zazzafan numfashi mai cike da tururun zuciya da tarin baƙin ciki.
Ita kuwa Ummeey a hankali ta ƙara matsowa kusa dashi hannunta ta ɗaura tsakiyar kanshi tare da tura yatsunta cikin sumar kanshi tana mishi wani irin shafawar dake ƙara tunƙuɗo hawayenta da nashi a lokaci ɗaya.

Ita kuwa Afishan sabbin hawayensa dake ƙara kwaranyowa ta ci gaba da sharce mishi da ƴan hannayenta murya na rawa tace.
“Abeey to ka daina kuka, in baka yi fushi da niba, kuma ka yafe min”.
Lumshe idonsa yayi tare da ci gaba da magana cikin murya mafi ƙololuwar rauni.
“Ki daina kuka Afishan Abeey bazai taɓa yin fushi da keba, bare in gaza yafe miki, duk girman

laifin da zakiyi min koda kuwa ance min kinyi hatamtaccen abune, dan nafi kowa na duniya sanin halinki nasan abinda ko sau dubu za'a gaya min ƙaryane bazan yarda bama dan. Bazan iya nesanta kaina da keba, My happiness.”
Sai kuma ya ƙara tallabe fuskantar cikin tafukan hannunsa tare da taune lips inshi duka biyu. Murya na rawa yace.

“Shi yasa nake roƙon Allah da kada ya barni a raye in dai akwai ƙaddarar da zata zo tasa inyi fushi dake ko ɗaya daga cikin yarana, gwara in mutu kafin zuwan wannan lokaci.
Gwara kuyi kukan maraicin rashina a duniya, da in ƙunsa muku azabar baƙin cikin nesantaku dani da mahaifiyarku, dan na sani duk duniya baku da ababen so sama dani da mahaifiyarku.”

Cikin tsananin tausayi Hamisu ya rumtse idanunsa da ƙarfi saboda jin hawayensa na tsiyaya.

Shi kuwa Tajj murya cike da rauni da sanyi da rawa tamkar mai jin sanyi yaci gaba da mgnar cikin kukan da yake son danne wa kuma yaƙi dannuwa.

“Dan haka na yafe miki Afishan Abeey”.
Da sauri ta faɗa jikinsa, shima ruggume ta yayi tsam a jikinsa.
Tana kuka tace.
“Abeey bazaka mutuba!”.
Da sauri shima yace.
“Afisha ai mutuwa dolene”.
Tana ɗago kanta a jikinsa tace.
“Abeey zan roƙi Allah ya ƙara mana lfy da rai da nisan kwana”.
Sai kuma ta koma gaban Ummey kema ki mishi addu'a.
Cikin kubcewar kuka Ummey ta fara magana.
“Allah ya ƙare min kai ya ƙara ma lfy da nisan kwana mai amfani, Allah ya rayaka akan yaranka ya rabani da ganin mugun abu.
Afishan zaki rayu da Abbanki insha Allah”.
Wasu irin numfarfashi da sheshsheƙan kukan ne ya kubce mishi, wanda yasa gaba ɗaya jikinsa fara wani irin karlarwa alamun zazzaɓi na gab da mishi dirar mikiya.

Sai kuma ya miƙe da sauri.
Yana faɗin.
“Amin Amin Ameeeeeeeen ya rabbil alamin”.
Sai kuma ya jawo hannu Afisha tare da cewa.
“Afisha mu tafi”.
Da sauri Ummey ma ta riƙe ɗaya hannun Afisha.
Sai kuma ta miƙe tsaye tare da ɗago kanta idonta ta zuba cikin nasa yau shekaru tara kenan rabonta da sa ɗanta a idonta.
Kawai sai ta ruggumeshi tare da sakin wani kukan tana  faɗin.
“Muje Afif na haƙura, bazan sake jurar nesanta da kaiba na haƙura da auren mutum mai azzalumar zuciya mai raba uwa da ɗanta mu tafi, daga yau duk inda kake ina nan.”

Ruggumeta yayi shima yana jin ɗumin jikinta da yake bege, kai ya fara jujjuya mata tare da cewa.
“Kiyi haƙuri Ummey ki zauna da shi ko dan gudun kada tsinuwarsa ta kamani”.
Da sauri tace.
“Afif ina sonka ina son Afisha ina son rayuwa da ita wuri ɗaya dasu Ayeed”.
Da sauri ya saki hannun Afisha tare da cewa.
“To Ummey na gashi na bar miki ita ku kwana da safe Hamisu zai zo ya ɗauketa”.
Sai kuma ya sunkuyo ya kalli Afishan tare da cewa.
“Kina son zama anan?”.
Da sauri tace.
“Eh Abeey ina son Ummeey da Yah Abana Amman ka dena kuka”.
Ta ƙare mgnar tana sakin wani kukan tausayin ganin mahaifinta na kuka.

Da sauri ya rumtse idanunsa tare da juya kansa ya kalli inda Yah Abana ke zaune.
Cikin wani irin maraitacccen kukan daya kubce mishi ne ya nufi waje da sauri harda sassarfa.
Da sauri Hamisu ya rufa mishi baya.

Ita ma Ummeey da sauri ta kamo hannun Afisha tare da juyawa ta rufa musu baya.
Sai kuma ta juyo jin Yah Abana ya riƙo hannunta tare da cewa.
“Ina zakije? In kin fita ban yafeba”.
Cikin watsa mishi wani irin fusataccen kallo tace.
“Ka sakeni Muhammad wallahi yau ba abinda zai hanani bin ɗana kada Allah yasa ka yafe ɗin, ni bana ma buƙatar yagiyarka ko ka mance cewa yanzu ni ba matarka bace”.
Dai-dai lokacin kuma Hamisu dake bayan Tajj da tuni ya fita shima ya fice tare da jan ƙofar ɗakin.
Shi kuwa  kuwa Yah Abana cikin rumtse idanunsa yace.
“Inji uban waye yace ke ba matata bace”.
A fusace Ummey tace.
“Inji kai Uban Afif, Maryam, Rashida, Halima, da Zakiya ko ka mance cewa kayi duk randa nayi alaƙa da Afif ko na kira sunansa akan igiyoyin aurenmu.
Shi kuma in ya kuskura yazo inda nake akan aurenmu kuma ka baka yafeba kuma kace zaka tsine mish.”
Da sauri yasa tafi hannunsa ya rufe mata bakinta.
Idonunsa dake kwaranyar da hawaye tamkar an ɓalle kan pomopm ya rumtse da ƙarfi tare da fara magana cikin murya mafi ƙuna yace.
“Na janye wannan furucin tun ranar  Matar Abbana ta haifi yarsu ta huɗu Daddey. Na yafe miki kuma ban sakeki bakiba.
Shi kuwa Afif wai ke kika haifa min shine?!”. Sai kuma kawai ya jawota jikinsa tare da Afisha ya haɗesu ya ruggumesu tsam-tsam tamkar zai haɗiyesu dan yaji ya rasa kalaman faɗa mata....!

Tsaya-tsaya fa kiji yar uwa.
Zuwa yanzu na gama nazari da fahimtar ƙorafe-korafen wasu daga cikinmu mata da kan zomin

da kukansu ire-iren haka👉

Garkuwa mijina baida kuzari!
Garkuwa mijina yana fin sati biyu ko uku bai buƙaceni ba!.
Garkuwa mijina baya gamsar dani in an fara 2 minute yakeyi.
A'a Garkuwa wlh abin oga yana ƙanƙancewa.
A'a Garkuwa saifa muna cikin hidima abu yayi bacci.
To ku taho ku kuma yi shiru.
In sha Allah, da yardar Allah da kuma izininsa da faɗinsa bai sauƙi ko wanne ciwoba Saida ya sauƙi maganin cutar, sai dai in ba'a ganoshi ba.
Yar uwa kizo da yaƙini da yarda in Sha Allahu kukanki ya ƙare.
Domin akwai haɗin maganin maza.
Na basir da sanyi.
Domin mafi akasari matsala biyun nanne ke sasu wannan matsalar.
Bayan maganin matsalar kuma, akwai zazzafan haɗin maza.
Mai magance matsalar ƙanƙancewar gaba, mai ƙara masa kuzari, da girma, gami da iya juriyar daɗewa lokacin raya sunna, da samawa iyali gamsuwar da zata ƙara zaman lfy da inganta farin cikin dararen ma'aurata.
Akwai maganin na gargajiya da kuma na Bappa Nasara ke dai ga Number ta 08069423567 kimin magana in kin san a shirye kike zaki saya. Ga kuma account no na nan 0005388578 Jaiz bank Aisha Aliyu Garkuwa.

By
*GARKUWAR MARUBUTA**INDA RAI*
Part 3  Page 4
Na
*Aysha Aliyu Garkuwa*

Alamomin infection sune kamar haka. Rashin sha'awa. Ƙaiƙayin gaba Kiji idan ya fara miki ƙaiƙayi kamar zakiyi hauka. Warin ko ƙarnin wurin. Fitar farin Ruwa mai fatsi-fatsi. Ƙurajen su ɗan fetso ƙananan ko ƴan manya, melewar fatar wurin, Tusan gaba. Bushewar gaba, Rashin ni'ima. Buɗewar gaba, domin har budurwa infection na iya buɗata. Ciwon mara ko ciki mai tsanani yayi al'ada, rashin haihuwa, domin har baƙin mahaifa take toshewa. Ko kirinƙajin wani abu na miki yawo ƙasan mara, ko jin zafi yayin yin fitsari, da kuma sdw, da dai sauran abubudann ban  lissafa Sune manyan alamomin infection.

Shin kin kuwa san illar da infection keyi miki, amman kinajin ɗaya daga cikin alamominta kinyi bulum buƙui da ita a jikinki. To bari kiji illolin infection wato cutar sanyi.
Rashin haihuwa, ƙyara da hantara a wurin miji domin muddin kina tare da ita baki da wata daraja a idanu nai, sabida ƙyamas kike ba damshi bare wata ni'ima mai Taste, Kinga kenan shinfida ta lalace, in kuwa shinfiɗa ta lalace dole kiga sauyin fuska, domin su maza dole

sunason wurin da kwaranya, zaki kasance baki da wani daɗi da ɗumin da mai gida ke buƙata. Kinga duk tsabtarki da kyanki da iya girkinki shinfidarki ta zama lami. Kiyiwa Allah ki nemawa kanki lafiya ki samawa mijinki da ke kanki nitsuwa.

KADA KUJI IYA WANNAN DOMIN AKWAI MUGUN INFECTION WANDA BAYA BAYYANA KANSA. Wanda kawai sai dai kijiki, kamar kwalta kin bushe ƙyamas ya dauke miki dukkan sinadaran ni'imomin ki, da sha'awarki, duk kayan matan da zakisha a wofi zadai kiji ƴan uwa da abokan arziƙi da ƙawayenki na yaba miki magunguna GARKUWAR MA'AURATA, amman ke in kinsha jiya I yau,  duk nacin oga da yi miki wasannin bazaki ji sha'awa ba, toh wlh muguwar infection ce, wacce bata bayyana kanta har sai ta gama yi miki rugu-rugu. Ta lalata miki zaman aure. Lokacin da zata bayyana sai kiji Doctor's suna kira miki, ovarian cyst, ko kuma fibrod duk a cikin chronic infection ne yar uwa.

INFECTION set ɗinmu na kowa da kowane Mata, Maza, Bazawara, Budurwa, Maijego, Yara, Ke yar uwa Wlh har maiciki zatasha, bashi da matsalar komai Maganin na Gargajiya ne mai rakake INFECTION ya fito miki dashi, wlh duk nacin infection koda na cikin mahaifane bi'izinillahi ta'ala zaki rabu dashi, cutar infection cutace mai masifar naci, so yar uwa kana dole ki nace masa da maganin set ɗin na 10k ne kuma maganin kala biyarne nasha da kala uku na tsarki ɗaya na shafawa ɗaya. Yar uwa idan har kin saya to kiyi ƙoƙarin kisha da mijinki, in akwai abokiyar zama, kisa miji ya saya mata, domin ko kin rabu da shin dai ita tana dashi tofa kin kashe macijine baki cire kaiba, ma'ana zai sake dawo miki,

idan kuna da yara suma a saya musu, domin tsoron kada ya riƙa a jikinsu musamman ya'ya mata ya buɗa miki ƴa tun tana ƙaramarta, ki aurar da ita miji na muku kallon lalatattun iyaye da baku iya bada tarbiyaba. Saboda yamayin garin yasa ina raba rabin set ɗin in sa miki komai rabi-rabi 5k amman na ɗan saki Garabasar 4k set ɗin 10k ne Amman yau 8k ne. Idan kin san a shirye kike ga account number na nan 0005388578 Jaiz bank AISHA ALIYU GARKUWA, ki turo kuɗinki kafin kiyi min mgn ta WHATSAPP NUMBER'N na 08069423567 sai ki turo min shaidar biyanki, domin akwaishi Available ko yau kika tura kuɗinki, gobe kayanki zai taho, ina bada sari ko sayan ɗaɗɗaya. Farashin Sari da sauƙi daga kan mutum 3 ko 6 ko 12. Kai ko na mutum 24 kikeso in Sha Allah zaki samu ina kuma bada sarinsa a farashi mai sauƙi.
Please dan Allah in dai kinsan baki shirya sayaba kada kimin mgn ki bari sai kin shirya. Taku ce dai GARKUWAR MA'AURATA

Dan Allah in dai kinsan baki shirya sayaba kada kimin mgn, masu cewa wai sun goda suga number'n nayine, ko kuma a'a bari dai in na shirya zan sake miki mgn, ko kuma yanzu dai kuɗin bai cikaba tukun sai sun cika, ko kuma a wanne gari kike, kai munyi nisa, toh  ai duk nisan state da kike ba ruwan mota ba inda bazai kai mikiba, nake turawa ƴan ƙasashen wajema. Kuyiwa Allah da Manzonsa in dai in kinsan Baki shirya sayan kaya ba kuyi haƙuri kada kumin mgnar ku bari sai kun shirya,kada kuzo mu ɓatawa juna  lokaci Allah y sani na tsani bana son mutum yaga na mishi ba dai-dai ba nima Kuma bana so ayi min wasa da hankali a harkar kasuwanci 🙈🤗🤣, duk bayani na gamayi in dai saya zakiyi ga kuɗin kaya ga account no ga numberta ai sai ki biya kawai kafin kimin mgn. Tunda dai ga alamominshi duka.

Da sauri Addawa ta miƙe tsaye tare da zubawa Hamisu ido, tare da nufowa inda yake dan gani take kamar baya saurin shigowa.
“Ina Afif ɗin? Kunje ɗin ne? Me Abbanshi yace? Ina Afishan? Shi da waye ne yazo. Abban Afif ɗin ya tsine mishi ko?”.
Wani irin sassayan numfashi Hamisu ya fesar tare da Lumshe idonsa kana ya buɗesu yana mai riƙo hannunta yace.
“To Addawa wacce tambaya ɗaya zan fara amsa miki”.
Cikin kaɗuwa da tarin fargaba tace.
“Duka, kai ina Afif ɗin?”.
Ɗan guntun murmushi gefen baki, mai cike da tausayin Afif ɗin yayi tare da cewa.
“Kwantar da hankalinki Addawa, Yah Afif yana Ify, tare muka dawo ya haura sama, kuma Afisha na can, Ummeynshi tace ya bar mata ita, Yah Abana kuma bai tsine mishi ba, kai ko mugun kallo ma bai mishiba Kum...”
Sai kuma yayi shiru tare da juyawa da sauri ganin ta raɓa ta wuce shi, ta nufi sama wurin Afif ɗin.

Kai ya jinjina cikin gamsuwa da so irin na kaka da jika.

Sai kuma ya nufi ɗakinsu Laylah inda yake jiyo alamun Muryar ta tana bitan.
Ƙofar ya tura tare da ɗan jingina ta gefe yana mai kallon Ayeed da Ayaan da sukayi bacci ruggume da sawun juna, kan Ayeed na ta sawun Ayaan.
Da sauri Rahman ta ɗago kanta ganinshi tsaye ya dawo da kallonshi kanta ne yasata sauƙe numfashi mai nauyi dake ƙara kafa sonshi a ranta tace.
“Ya dai ina Afisha, Abeey ya huce”.
Kwaɓe fuska yayi tare da cewa.
“Hayateeh Yunwa nakeji, kizo muje ki bani abinci kafin in amsa miki”.
Miƙewa tsaye tayi tare da cewa.
“Ba'afa ɗaura aurenba tukun”.
Longoɓar da kansa yayi tare da cewa.
“To barni yunwa ta kasheni ki huta”.
Da sauri tace.
“Allah ya rufa min asiri, ai ciwon zaimin yawa a raina, na rasa uwa, uba, yayu, ƙani, yanzu kuma kamin fatan rasa miji, abokin rayuwa, jigon farin cikina, uban yayana In Sha Allah”.
Ta ƙare mgnar a lokacin da suka zauna kan Dinning table ɗin.
“Allah ya bamu tsawon rai da Ify da zuriya ɗaiyiba mu samu irinsu Afisha”.
Tana zuba mishi abinci a plate tace.
“Amman dai kamin alkawarin ba kishi ya ko”.
Kai ya jinjina mata.
Da sauri tace.
“Yauwa kuma ga ƙarin wani alkawarin duk laifi banda mari irin na Abeey”.
Tsuke fuska yayi tare da tsareta da ido cikin isar matsayi irin na mijin gsky yace.

“Itama Ammeey ita ta jawo ya mareta, duk da nagartarsa saida ta ƙureshi tasa ya kai hannunsa jikinta, Yah Afif ma yayi mari da akayi mishi wargi akan yaransa shi da yake ma nagarci mai tsananin haƙuri  gautsin bakinta da taiwarta yana faɗa tana faɗa ya ja ya mareta, bare ni Hamisu da haƙurina bai kai nasaba, in bakya son mari kada ki kwatatanta yin abinda yar uwata tayi a yau, dan in nine ya Afif ma sai na haɗa mata da Hangurɓar kumbura mata fuska da mari in fasa baki da naushi in karya ƙafa”.
Da sauri ta miƙe tsaye tare da zazzaro idonta waje tsoronta ya fito a fili, sai kuma ta koma ta zauna jin ya jawo hannunta ya zaunar da ita tare da cewa.
“Amman ke a ganinki abinda Ammey tayi ta kyauta?”.
Cikin sanyi tace a'a.
Murmushi yayi tare da sakin fuska kana yace.
“To kada kiga laifin Yah Afif. Hayateeh ke nasan ma bazakiyi min hakaba koma mun ɓata ba laifi bane, dan tsaɓanin masoya hutune kuma in an shirya sai danƙon so ya ƙaru kiga anfi ji da juna, yanzu mu zuba musu ido muga fushinsu da shiryawarsu zakiga bayan nan sai sun nemi haɗiye juna a gabanmu.
Amman kafin nan akwai zaman ƙunci a gidan nan dan naga duk sun fusata”.
Tana murmushi tace.
“Ai shi zaizo ya bata haƙuri”.
Da sauri yace.
“A'a itace zata bada haƙuri dan itace mara gsky”.
Cikin sauƙe numfashi tace
“Anya kuwa?".
Yana juya spoon ɗin hannunsa yace.
“Zamu gani dai”.

Addawa wace durƙushe gaban Tajj tayi sujulshukur saboda jin harda ɗiyarta aka zo kuma Yah Abana bai tsine mushi ba, sai kuma ta zuba mishi ido ganin har yanzu hawaye ne ke kwaranya a idanunsa lips inshi na rawa alamun so yake ya danne sheshsheƙan kukan dake son fuzgo mushi.
Idanun sunyi jazir jiyoyin kansa duk sunyi ruɗu-ruɗu more especially na kan goshinsa cikin rawan murya yake cewa.
“Addawa sujjadar Godiya a tabbatar tsinuwar Yah Abana a kaina, Addawa sujjadar Godiya a tabbatar mutuwar auren Ummeyna sujjadar Godiya a tabbatar Allah ya isan Yah Abana ya hau kaina tunda yau duk na keta alfarmarta ƙa'idar da yasamin na kar ya ƙara ganina a duniya kar in kuma zuwa inda yake”.
Sai kuma yayi saurin kife kanshi bisa kujerar da yake zaune a gabanta tare da kubcewar kuka.
Da sauri Addawa ta zauna bisa kujerar, kanshi ta ɗago tare da ɗaurawa kan cinyarta tafinta ta kife a kan kafaɗunsa tana ɗan bubbugawa, cikin Muryar tsammani tace.
“In sha Allah babu tsinuwa a kanka, kuma ba Allah ya isa a kanka, kuma da yardar Allah auren mahaifiyarka na nan daram.
Tajj kayi shiru ka fahimta mana shine fa da kansa ya nemeka”.
Da sauri ya ɗago kanshi tare da cewa.
“No Addawa Afisha ya nemafa ba niba, kiɗima tasa na mance naje”.

Hannunta tasa tare da tallabe fuskarsa kana tace.
“To ai duk wanda ya nemi Afisha kai ya nema, duk wanda yaso ganin Afisha ai kai yaso gani.
Saboda duk wanda yaso ɗanka to kai yake so.
Tajju ai kaine Afisha”.
Da sauri yace.
“Ki fahimta Addawa nifa da naje har na bar wurin ko ɗago kanshi ya kalleni da idanunsa baiyiba.
Ina jin ƙamshin jikinsa da na rasa ji tsawon shekaru tara, ina ganin sawunsa da kullum in ina kusa da shi yake ɗaura kaina a cinyoyinsa.
Ina kallonsa inaji bege da sha'awar ya jani jikinsa ya ɗaura kaina a cinyarsa yasa tafin hannunsa na dama a tsakiyar kaina yayi min Addu'a yasa min al'barkar da nayi missing nata tsawon shekaru tara in yi mishi massaging sawunsa da nayi shekaru tara ban mishi.
Addawa duk fa bai bari na samu wannan ladan ba, ko kallona baiyiba ko sunana bai kiraba, ina son inji yace min.
Abbana Amman yaƙi.”
Sai kuma kawai ya fara bubbuga gefen kanshi da hannunsa na dama yana faɗin.
“Addawa nayi asarafa a rayuwata tsawon shekaru tara cikin fushin mahaifi kuma ba sa al'barka uwa, kuna ga kamar na rabu da baƙin cikin rashinsu a kusa ko, yana raina fa”.
Da sauri tace.
"Innalillahi haba Tajju kayi Astagfirillah, na sani kullum Fatimana tana saka maka al'barka ta kuma yi maka addu'a a cikin dukkan motsinta ai shiyasa kake samun nasara, shi kuma mahaifinka ai bai tsine makaba bai kuma ja maka Allah ya isaba tunda yasa sharadin sai kaje inda yake ne ko kayi alaƙa da yayansa da mahaifiyarka.
Kuma ka kiyaye bakayi ba,
Wannan shine sirrin nasararka da rashin ganin masifa, ai ba don wannan ba ko da gskyarka iyayenka suka fushi da kai sai kaga ba daɗi.
Kuma zuwa Yah Abana Qatar da neman Afisha ai duk shimfiɗar son ganinka ne.
Kuma zaka gani da idonka, Addu'ar da mahaifiyarka keyi kullum ne lokacin amsashi yazo, in sha Allah asirin magauta zai tonu nan kusa inaji a jikina komai zai bayyana nan kusa gsky zatayi halinta, jifan da sukayi yana gab da sauƙowa ƙasa bayan tafiya sama da yayi tsawon shekaru tara, dan duk nisan jifa ƙasa zai faɗo”.
Sai kuma ta ƙara tallaɓe kanshi da kyau tare da fara sharce mishi ruwan hawayensa.
“Kai da Allah ya baka ajiyar ƙura'ani mai girma a cikin kanka ai kuka bai canceka kaba, yi uziya da basmala fara karatu nasan shine abi mafi daɗi da sauƙin samar da warakan ko wanne ciwo”.
Ai kuwa kamar mancewa yayi ta tunasar dashi.
Cikin lumshe idonsa ya fara karatun tun daga farkon Alkur'ani mai girma.
Da ƙarfi ya sauƙe wani zazzafan Ajiyan zuciya lokacin da ya dire ayar karshe ta Suratul fatiha, kana ya ɗaura da suratul Baqara.
Gyara zama tayi har Saida taji ya kai tsakiyar surar kana ta miƙe ta fice.
Baima san ta fitaba dan falalar Alkur'ani tasa baya jin komai sai sautin muryarsa da kuma sauƙe Ajiyan zuciya akai a kai.

Ita kuwa Ishmah tunda ta shiga ɗakin ta faɗa kan gado, ta ruƙume Daddey ta saki wani irin maraitacccen kuka mari a gaban kowa da kowa na gida zai dakeki akan yar da kika haifa a

cikinki.
abinda shaiɗan ke karanta mata kenan haka ya ƙara ingiza fushinta da ƙunar ranta tai ta Kuka har bacci yayi awon gaba da ita, tana mai jin raɗaɗin marin sai ajiyar zuciya take sauƙewa.

Shi kuwa Tajj ranar haka ya kwana karatun Alkur'ani ko na second ɗaya bai rintsaba.

Washe gari misalin ƙarfe takwas dai-dai tsaye take a dannin area cikin disashewar murya ta kalli Laylah dake tsaye gefenta.
“Ki ɗauko mayafinki ki zo ku kaiwa su Yah Abana breakfast.”
Ta ƙare mgnar tana nuna mata basket har biyu da suke kan dinnin table ɗin.
Cikin sanyi Laylah tace.
"Toh Ammey”.
Sai kuma ta juya ta nufi ɗakinsu tana mai jin tausayin Ishmah sabida ganin yadda fuskantar ta kumɓura tayi jazir more especially gefen hagunta inda nan ya bawa maruka biyu, ya kumbura sosai hatta shatin yatsunsa na kwance ras, kana cikin gefen idon ya tara jini kamar irin wacce aka tsole da ƙarfi haka.
Gashi kuma duk idon suma sunyi jazir ga muryarta dake a disashe saboda kukan da rasha.

Haka nan taji hawaye na cika mata ido.

A inda ta barta a nan ta dawo ta same a tsaye.
Basket ɗin ta ɗauka duka biyu tare da cewa.

“Ammeey kice Ayeed yaje ya kira Yah Hamisu.”
Kai Ishmah ta jinjina tare da cewa.
"Muje in kira miki shi”.
Domin ƙa'idar gidan ne yara mata basa shiga ɗakin mazan.
Shiyasa Laylah barata jeba.

"Yauwa gashi nan ma”
Laylah ta faɗa lokacin da suka fito cikin corridor.
Da sauri ya amshi basket ɗin yana kallon yar uwar tasa.
Da sauri yayi ƙasa da kansa saboda ganin yadda fuskantar da idonta suke, lokaci ɗaya ƙauna da tausayin yan uwan takan suka motso lip inshi na ƙasa ya ɗan taune tare da cewa.
“Adda muje in kaiki hospital ki samu magani”
Kai ta jujjuya cikin sanyi tace.
“Lafiyata ƙalau ɗan uwana kuje”.
Ta ƙare mgnar cikin kauda kai tare juyowa ta koma ciki.

Cikin sauƙe numfashi ya ɗan kalleta lokacin da suka fita daga harabar gidan.
“Hayateeh kuka kikeyi?”.
Cikin sanyi tace.
“Yah Hamisu kalli fuskar Ammey nafa”.

Kai ya ɗan kauda dan kar ta gane raunisa cikin sanyi  da iya kar gsky yace.
“Kawai dai hannun Yah Afif nada tsananin zafine ita kuma abu da farar fata, shiyasa tayi haka, da Ni ya mara da fuskata bazatayi hakan ba, kuma in sha Allah itama zai watstsake”.
Cikin sanyi tace.
“Ayyah Ammeyna kusan kwana kuka tayi fa”.
Yana ɗaukar hanyar da zata dasu da hotel ɗin yace.
“Dama haka take da raki da saurin kuka”.

A can cikin gida kuwa.
Cikin kulawa da tausayi Addawa ke kallon Ishmah dake ƙoƙarin komawa kitchen tace.
“Me kuma zaki koma kiyi a kitchen”.
Murmushin ƙarfin hali tayi dan ciwon kai dake damunta ya fara sata jin bata son surutun a hankali tace.
“Zan fara haɗawa su Ummey lunch ne”.
Cikin sanyi da tausayi Addawa tace.
“Kiyi haƙuri kizo kiyi breakfast, Kisha magani ki kwanta ki huta, ni da kaina zan shiga kitchen din da Zulaihat in musu lunch ɗin”.
Da sauri tace.
“A'a Addawa barini in samu ladan mana”.
Miƙewa tayi da sauri tace.
“To naji Amman dai zo Kisha ko tea ne sai kisha maganin”.
Dole tabi Addawa tea ta haɗa mata da kanta kana ta bata tasha tare da maganin.

Cikin wani irin matsanancin farin ciki Ummeey ta rugume Laylah da ƙarfi tare da cewa.
“Allah sarki Laylah kece haka”.
Ita kuwa  Laylah lip tayi a jikin Ummeeyn tana mai murmushin dake bayyana tsananin jin daɗin ganinta.

Hamisu kuwa da sauri ya ajiye basket ɗin tare da rugume Afisha.
Dake tsalle musu oyoyo.
Cikin girmamawa Hamisu ya kalli Yah Abana da yace.
"To ai zaki kada Uncle ɗin, sakeshi ya zauna”.
Da sauri ta sakeshi sai kuma ta ruggume Laylah.
Shi kuwa Hamisu cikin girmamawa yace.
“Barka da safiya Yah Abana”.
Kan Hamisun ya shafa tare da cewa.
"Barka dai an turoku ɗaukan Afishane da sassafen nan?”.
Da sauri yace.
“A'a Yah Abana Adda Ishmah ce tace mu kawo muku breakfast”.
Ya ƙare mgnar yana nuna mishi basket ɗin da ya ajiye.
Kai ya ɗan sunkuyar ƙasa tare da cewa.

“Allah yayi mata al'barka.”
Cikin jin daɗi Hamisu da Laylah sukace.
“Amin Yah Allah”.
Yana jawo Afisha jikinsa yace.
“Ya baku kawo min Ayeed da Ayaan ba?”.
Da sauri Laylah tace.
"Sun maida bacci basu san zamu zoba.
Ayeed tun jiya fushi yake wai an hanashi zuwa.”
Ta ƙare mgnar tana tahowa inda yake dan yafitota da yayi da hannun sa.
Gefenshi ya nuna mata a ƙasa.
Da sauri ta zauna tare da kallon Ummeey da ke cewa.
“Ina Addawa na, ina Ammeyn naku da Daddey”.
Cikin yar sakekkiyar murya Yah Abana yace.
"kice ina Hayateeh Daddey na”.
Da sauri Afisha ta kwaɓe fuska tare da cewa.
“Daddey ne Hayateenka”.
Murmushin su Hamisu sukayi dan sun san Afisha kullum cewa take wai gani take da kamar Dadeey akafi so.
Kanta Yah Abana ya shafa tare da cewa.
“Ke My happiness Daddy kuma Hayateeh”.
Da sauri tace.
“A'a ni dai Hayateeh nake so, ai sai an rayu kafin ayi farin ciki gwara dai ni in zama rayuwarka ita kuma farin cikinka to su Ayeed fa”.
Dariya suka watse dashi har Yah Abana saida ya ɗanyi murmushi mai sauti kana yace.
“To Hayateeh haka za'ayi Ayeed da Ayaan kuma friends  nane ai”.
Murmushin dake nuna wani irin mashahuran farin ciki ma bayyani Ummeey tayi tare da cewa.
“Wallahi ina son ganinsu fa Malam”.
Cikin lumshe idonsa yace.
“Zaki gansu in sha Allah”.
Da sauri tace to sai yaushe”.
Yana ɗan shafa kan Afisha yace.
“Verry soon”.

Dubai.
Tuni hall ɗin ya cika yayi maƙil.
Yaran ƙasar Japan da China aka fara haɗawa, suka goga a fagen rawan.
Inda Chaina ta kora Japan gefe.
Nan
Kuma aka haɗa Ethiopia kuma Mali.

Cikin abinda bai gaza awa biyu ba Yasir da sauran yan tawagar sukayi waje da ƴan Mali.
Haka dai suka ci gaba da fidda gwaneye, a ranar aka yi tantancewar forko gobe kuma za'a ci

gaba da rairarye gwanayen kasashe.

A hankali yake fesar da sassayan numfashi tare da shaƙan dadɗan ƙamshin da parlon ke zubawa, idonshi ya ɗan lumshe kana ya buɗesu a hankali tare da tsaida kallonshi kan gefen fuskantar da yake ɗauke da shatin yatsunsa da sukayi ruɗu-ruɗu sunyi jazir.
Lip inshi na ƙasa ya ɗan ciza ta gefe tare da ɗaura tafin hannunsa kan cikinsa da yakejin yana kukan yunwa da rabonsa dasa abi a bakinsa tun jiya da asuba da zai taso, nanma iya tea yasha.

Zura hannunsa ɗaya yayi cikin Jallabiyar dake a jikinsa sky blue color sai wani irin Ni'imataccen ƙamshin da yake bazawa, wanda ya rigada ya kama jikinsa.

Ita kuwa Ishmah tunda ya shigo kanta ke sunkuye tanayiwa Daddey kitso duk da manyane, sanye take cikin doguwar rigar material sky blue color sai ratsin Pink and red color.
Rigar tayi cas a jikinta duk da ba wata kwalliya tayi ba Amman tayi masifar kyau, sai ƙamshin kullacar sirri da shu'umar humra take bazawa yanayin jikinta kuwa cike yake da rauni.

Hmmm! Addawa tayi gyaran murya don ganin tunda ya shigo bai zauna ba, kuma bai cire idonsa kan Ishmah ba, ita kuma bata ɗago kai ta kalli inda yake bama.

“Zauna mana”.
Tace tana kallon Zulaihat da ta fito daga kitchen ta nufi ɗakinsu Ayyed dan tada su a bacci tayi musu wanka.
Bisa alamun ta gama gyara komai na abinda Ishmah tayi amfani dasu wurin girkin rana da wanda za'a kaiwa su Ummeey.
Yana mai rumtse idanunsa ya zauna gefen Addawa tare da amsa gaiduwarta.
“Muje kuyi breakfast ko?”.
Addawa ta faɗa tare da miƙewa.”.
Kai ya jinjina alamun to.

Da sauri Addawa ta kalli Ishmah data miƙe tsaye tare da tallaɓe Daddey a jikinta ta juya ta nufi ɗakinta.
“A'a Ishmah ina kuma zaki tafi, ki kwantar da ita kizo muyi breakfast ko?”.
Ba tare da ta kallesu ba murya cike da rauni can ƙasa a narke tace.
“Bismilla kuci kawai Addawa bana jin yunwa”.
Cikin kulawa da jin tausayi Addawa tace.
“Me kikaci da zakice bakya jin yunwa, tun jiya da safe fa raban da kici abinci haka kika wuni kika kwana da yunwa, dan Allah kada muyi haka dake Ishmah, kiyi haƙuri kizo ki kwantar da Daddey anan muci abinci”.
Cikin murya mai tafe da rauni tace.
“Kiyi haƙuri Addawa ba ɗazu kin bani tea ba, wallahi Allah bana jin yunwa kuci kawai, bazan iya cin komaiba”.
Miƙewa yayi ba temare da ya kallesu ba ya fara tafiya zuwa Dinning area.

Itama Addawa numfashi ta fesar tare da juyawa zata bishi dan tunda taji ta rantse tasan to ko ya za'ayi bazata cin bane.

Ita ma Ishmah a hankali ta juya dan nufar ɗakinta.

Kamar daga sama haka suka ga Afisha ta shigo parlor a guje tare da rakadi tana faɗin.
“Hello Ammey! Ammey!! i miss you Ammey”.
Dai-dai lokacin kuma ta ƙaraso gaban Ishmah tare da rarumarta da ƙarfi ta ruggume ta.
Irin ruggumar nan ta yara da take sa Mutun faɗuwa.

Da sauri Ishmah tayi taga-taga tare da dafe kujerar dake bayanta saboda saura ƙiris ta faɗi.
Cikin fusata ta hankaɗata gefe tare da yarfa mata wani irin zazzafan marin da yasa Afisha yin taga-taga ta faɗi gami da sakin wani irin maraitacccen kukan da yasa.
Addawa da Tajj da suka tsaya saurin nufowa kanta.
Cikin sauri Tajj ya tallaɓota jikinsa tare da miƙewa tsaye wani irin kallon ido cikin ido sukayiwa juna shida Ishmah cikin tsanani fusata da huci ya nuna ta da yatsa cikin fusakatacciyar murya yace.
“Ke wai meke damunki kanki ne?.
Me tayi miki  da zaki daketa?”.
Cikin watsa mishi wani irin kallo idonta na cikowa da hawaye tace.
“An daketa ɗin! Ko zaka rama matane? tunda kai kayi min dakon cikinta wata tara da kwana tara, ka kuma yi min naƙudarta da nishin haifa min ita kaji min zafi ketani da tayi ta fito duniya kuma ka shayar min da ita nace zaka rama matane?”.
Da sauri ya nufo kanta yana faɗin.
“Dan ke kika haifeta, sai aka ce Miki kece kika halicce ta ne?”.
Cikin zafin nama Addawa ta shiga tsakiyarsu tare da fara faɗin.
“Innalillahi wa innalillahi rajiun, aoozubillahi mina sharrin shaidan.
Tajjuddeen kada fa ka lizimci muguwar ɗabi'a akan fushi”.
Cikin zubda hawayen Ishmah ta fara mgnar cikin murya mafi rauni tace.
“Addawa barshi ya dakeni ai ya saba! baya jin daɗin rayuwarsa sai ya dakeni yake samun yayi numfashi mai daɗi!.
Barshi ya dakeni hakan shine riƙon amanar da Abbana ya bashi”.
Sai kuma tasa rafin hakan ta sharce hawayenta da wani ke korar wani murya a disashe taci ga da cewa.
“Abba na ya haifa ya bashi ne ai don ya daka kamar ya samu ganga.
Hakan shine yarda da yaƙinin da Daddey na tayi mishi kafin barinta duniya”.
Haka nan Addawa taji tuni kalamanta sun sa idonta cikowa da hawaye.

Shi kuwa Tajj jin kalamanta yake suna zubo mishi wani irin suka da suya a ranshi ji yake yi tamkar haɗashi da Allah takeyi kallon da take mishi ido na zubda hawayene yasashi yin ƙasa da kansa.
Ita kuwa Ishmah tana mai gyara riƙon da tayiwa Daddey tace.
“Ya ɗaukoni ya kawoni ƙasar da bani da kowa nawa domin yaci zarafina,

Dan haka barshi ya nuna ƙarfin ikonsa a kaina.
Na sani Ubangiji na zai min Sakayy..”.
Sai kuma sheshsheƙan kukan ya kubce mata.
Da sauri kuma tasa tafin hannunta ta rufe bakinta tayi shiru sabida shigowar Hamisu da Laylah.
Shi kuwa Tajj ruggume Afishi yayi kan guiwowinsa tare da shafa kanta yana mai jin kalaman Ishmah dake fita cikin tsananin rauni da rawan murya suna hukunta ruhinsa da jikinsa da ransa baki ɗaya.

Ita kuwa Ishmah da sauri ta share hawayenta jin Hamisu na cewa.
“Ammey ga Ummeey da Yah Abana tare muke dasu fa.
Kuma sunƙi shigowa.
Please Addawa zo ku shigo dasu“.
Wani irin Ni'imataccen murmushi mai nuna tsananin jin daɗi Addawa tayi tare da komawa ta zauna bisa kujerar dake bayanta tana mai sakin numfashi dake nuna tana da manufar zaman alamun bazata jeba dan tasan rashin zuwanta kamar akalar jawosu cikine.

Ita kuwa Ishmah da sauri ta miƙewa Laylah Daddy tare da juyawa ta nufu waje da sauri tana ƙara goge fuskarta.

Shi kuwa Tajj tamkar an dasashi haka ya kasa cewa komai sai shafa kan Afisha da yake yi yanajin kalaman Ishmah da na Hamisu na haɗe mishi.

A waje kuwa cikin wani irin mabayyanin so da girmamawa Ishmah ta buɗe marfin motar gefen da Ummeey take cikin Sassayan murya tace.
"Alhamdulillah yau gidanmu zai samu cikekken ma'anarsa na masu albarka da samun haske da darajar ziyarta iyaye mafi girma da daraja da ƙololuwar iya bada tarbiyya a duniya, yau muma zamu samu cikekken yaƙini da samun tsammanin albakar Ubangijin talikai tunda ga al'barka iyayenmu mafi soyuwa a garemu.
Bismillah Ummey ku shigo”.
Wani irin sassayan numfashi Yah Abana ke fesarwa tare da zuba mata idanunsa masu cike da sonta da yaranta.
Ita kuwa Ummey murmushi takeyi tamkar zata haɗiyi haƙorinta.
Sai kuma ta nunawa Ishmah inda Yah Abana yake alamun izininsa take buƙata.
Da sauri Ishmah ta zagaya daya gefen.
Cikin yin ƙasa da murya da girmama tace.
“Barka da zuwa Yah Abana, dan Allah Yah Abana shigo ko dan Addawa muma muci darajar Manzon Allah”.
Cikin kulawa Yah Abana yace.
“Sallallahu alaihi Wasallama”.
Ya faɗa tare da fitowa daga cikin motar”.

Wani irin sassayan numfashi mai haɗe da ruwan hawaye Ummeey ta fesar lokacin da suka shigo cikin corridor ɗin.

Ita kuwa Ishmah da sauri ta fara haura saman steps ɗin zuwa sashi mafi girma da daraja a gidan wato side ɗin Tajj.

Taka step ɗin forko tayi tare da buɗa muryarta cikin sauti mai cike da farin ciki take cewa.
“Addawa Laylah Ayeed Ayaan kuzo sama Addawa kuzo da sauri.”
Sai kuma ta kalli Yah Abana da Ummiey da idonta keta zubda hawayen.
“Bismillah Yah Abana Ummey ku taho”.
Cikin wani irin yanayi mai ratsa zuciya suka fara haurawa.

A parlor kuma da sauri Addawa ta kamo hannun Tajj da har yanzu yake tsaye,
Jawo shi tayi suka nufi wurin da Ishmah ke kiransu.

Yayinda ta yafito Laylah da Hamisun dasu Zulaihat da ta fito dasu Ayeed cikin shigar Jallabiyar sky blue color.

kusan duk a tare suke taka steps ɗin.

Su kuwa Yan Abana da Ummeey kan 3 sitter suka zauna tare da sakin numfashi a tare suna masu kallon tangamemen hotonsu dake kafe a tsakiyar falon wanda yafi tv falon girma.

Wani irin rawa da karkarwa jikin Tajj ya saki lokacin da yayi arba da Yah Abana da Ummeey a parlornshi a cikin gidansa a zaune a kan kujera.

Wasu irin zazzafan hawaye ne suka fara kwaranyowa mishi saboda ganin yadda Yah Abana ya buɗe masa hannayensa duka biyu alamun yazo ya ruggumeshi.
Cikin wani irin sassarfan da yafi kama da gudu gudu sauri-sauri, yazo ya faɗa jikinshi.
Cikin wani irin tsananin tausayi, ƙauna so, bege, kewa, rauni, gami da nadama mai zurfi Yah Abana ya ruggumeshi.......

By
*GARKUWAR MARUBUTA**INDA RAI*
Part 3 page 5
Na
*Aysha Aliyu Garkuwa*

*GARKUWAR* taku ce dai MA'AURATA, da masu shirin aure, da masu jego, da yan gayu masu son k'amshi kece raini, da gyaran da zaike  maimaita muku dararen forkon kuruciya*

Ko kunsan Jikinmu na da sinadaran hormones da suke taimakawa dan'adam akan komai musamman lokacin da mace take mu'amalar aure da mijinta. Mafi akasari wannan hormones din ne ke samun matsala ko su yi sanyi koma su daina aiki kwata-kwata shi ne dalilin da zai sa mace tace bata jin sha'awa ko bata san dadin aure ba. Albishirinku ina da kayan da ke taimakawa wannan sinadaran du dawo aiki tukuru don karkato miki da kimarki wajan mai gida sannan su taimakawa wannan sinadaran hormones dinki su dinka secreting din ni'ima wadatacciya da zata taimaka miki ki gamsu mijinki ya gamsu fiye da tunaninki. Note: Kayana ba sa tsinka ruwan ni'ima suna dai taimakawa hormones dinki ne su tsattsafo da ni'imar musamman wacca cutar sanyi ko dattin mahaifa ya dankarar da su ya hana su yin aikinsu yanda ya kamata. Haka zalika idan kina da kyau ki kara da wanka. Zaki iya amfani da magani na na gargajiya wanda zai gyara miki sex hormones din kullum ki kasance cikin humidify wato cikin damshi mai albarka kamar yanda ake son mace. Yana gyara miki mara.

Sai kamshi. Hajiyata daure ki fara amfani da turarena ki ji irin salon kamshin sa salo ne da zai daidaita ki da mijinki ya kankaro miki da kimarki a wajansa. Siyan na gari mayar da kudi gida.

Ga masu buƙata ga number' wayata wanda nake whatsApp dashi 08069423567 kimin mgn ta whatsApp in har kin tabbatar kin shirya saya mu dai-dai ta, kayana ba ƙanana bane, shiyasa bana harkan karanta, muddin kinsan baki shirya sayaba Please kada kiyi min mgn ki bari sai kin shirya kuɗinki a hannu,  ba ina nufin kayana bana talaka bane, no akwai ƙananan set na masu karamin karfi, banson aimin mgn a ɓatamin lokacin aiyukana a shirme baki shiryaba. Shine karantan da bana so.
0005388578 Jaiz bank AISHA GARKUWA ALIYU. In kin shirya ga number ta ga kuma account number ta wanda in mun gama mgn zaki turo kudin ki, kana insa miki kaya a mota, duk ƙasar da kike kayana zaije gareki, amman fa in kinada dalilin zuwan ce nasune🤝🏻sayan na gari meda kudi  gida....

Ƙam-ƙam ya ruggemishi cikin jikinsa tamkar wanda yake tsoron kada a kwace masa shi.
Shi kuwa Tajj sai kawai ya fara sakin wani irin sheshsheƙan kuka mai tsanyi da rauni wanda yafi kama da Ajiyan zuciya.
Ummey kuwa kawai sai ta zame ƙasa da durƙushe tayi sujulshukur kamar yadda taga Addawa tayi.

Suna ɗagowa kuwa kawai sai suka ruggume juna.

Afisha Ayeed da Ayaan kuwa da sauri suka isa inda Tajj ɗin yake suka kwanta a jikinsa da sauri Yah Abana ya ƙara buɗa hannayensa ya ruggumesu duka, sai kuma ya miƙawa Laylah hannun alamun ta miƙo mishi Daddeey,  da sauri ta muƙa mishi tare da zamewa ta zauna kusa dashi inda ya nuna mata.

Haɗesu yayi kab a jikinsa ya ruggemesu, tamkar wanda yake tsoron kada a kwace masa su sai wani irin dogon numfashi da Ajiyan zuciya yake sauƙewa.
Hawayen da yake riƙewane suka kwance mishi, hakan yasa yayi saurin sunkuyar da kanshi. Sai kuma ya fara shafa kan Tajj tare da ɗan bubbuga kafaɗarsa cikin Sassayan murya yace.
“I miss you so much Abbana, Allah yayi maka al'barka ya rufa maka asiri duniya da ƙiyama ya raya maka ahlinka. Allah ya ƙara dawwamar da kai cikin farin ciki da kwanciyar hankali Allah ya dauwamar da zaman Ify tsakaninka da Matarka yariyar kirki mai mutunci da karanci.”
Cikin murmushi mai tafe da hawaye Ummey da Ishmah da Addawa suke Amsawa da.
“Amin Amin Ameeeeeeeen Ya rabbil alamin”.
Cikin sauri kuma Ummey ta koma ta zauna gefen Yah Abana tare da yafito Ishmah.
Da sauri Ishmah tazo ta durƙusa gabanta tare da ɗaura kanta bisa cinyoyinta.
Hamisu kuwa mai raunin zuciya kamar mace tuni hotuna da vidio yake musu yana share hawayen dake zubo mishi.

Ita kuwa Ishmah cikin farin ciki mara misaltawa dan ji takeyi ta samu surka me zame mata madadin uwar data rasa.
Ummeyy kam shafa kanta take da sumbatar goshinta.
Sai kuma ta zuba idonta kan kuncin Ishmah da ya sha tarine Tajj, wanda har yanzu shatin yatsunsa ke kwance kana jan da fatar tayi bai washeba, cikin tsananin kula daso tasa tafukan hannunta duka biyu ta tallabo fuskar Ishmah tare da cewa.
“Ɗiyata meya ya sameki a fuska!?”.
Tayi tambayar ne cikin tausayawa.

Tambayar da tasa Addawa zuwa Tajj Ido shi kuwa Tajj da sauri ya kalli Ishmah cikin wani irin salon kallon da yafi kama da na ta rufa mishi asiri.

Wani irin kallon da yafi kama da bata son kallonshi ta watsa kishi tare da tsuke fuska kana ta dawo da kallonta kan Ummeyy murmushi tayi tare da kauda zance, ciki jin dadi tacewa Zulaihat.
“Zulaihat  tashi muje mu kwaso basket ɗin abinci su Ummeey da ma sauran duk womars ɗin abincin”.
Cikin girmamawa Zulaihat ta fice da sauri kuwa ta fara kawowa.

Ummeyy ido ta kuma dubawa Ishmah ta buɗe baki da nufin ƙara tambaya sai kuma taji Ayeed ya faɗa jikinta, haka yasa ta jawosu jikinta tare da cewa.
“Jikokina ababen so da alfaharina”.

Shi kuwa Tajj cikin sauƙe numfashi farin ciki ya ɗago kanshi tare da kallon Yah Abana sai kuma ya kalli Ummeyy, cikin jinsa tamkar yaron goye ya kwanta da kansa a tsakiyarsu cikin rawan murya yace.
"Yah Abana, ka gafarceni ka yafe min, ka ƙara min addu'a da yafiya, al'barkar nan bata isheniba, dan bazata goge fushin tsawon shekaru tara ba”.
Cikin sauri Yah Abana yace.
"Waya cema ina fushi da kai? Bana fushi da kai Abbana, Allah yayi maka al'barka ya ƙare min

kai da ahlinka baki ɗaya da muguwar ƙaddara".
Da sauri ya zame ya zauna ƙasa tare da jawo ƙafar Yah Abana ya ɗaura kan cinyarsa tare da fara yi mishi massaging sawunsa kamar yadda yake masa kullum in suna tare.
"Yah Abana ka yafe min? Ka amince inci gaba da alaƙantuwa da yan uwana? Ka yarje min inyiwa Ummeyna magana? Ka bani dama in sake haɗa sunana da naka? Ka amince ince kai mahaifinane? Ka dawo sani cikin yankaka? Ka janye sharaɗin da kai akan cewa in na matso inda kake ko na kula ahlinka akan auren Ummeyy na? Ka bani dama inje Ethiopia? Ka yarda in....".
Da sauri Yah Abana yasa hannunsa kan bakin Tajj ɗin kana ɗaya hannun kuma ya fara sharce masa hawayensa dake zuba cikin tsananin nadama yace.
"Na yafe maka komi da komai na yarje maka komi da kamai ɗana".
Da sauri ya juya ya fuskanci alƙibla yayi sujulshukur sai kuma ya kife kansa kan cinyar Ummeeynshi tare da ruggume sawunta sam.
"Allah yayi maka al'barka ya rufa maka asiri duniya da ƙiyama ya albakar yaranka".
Wani irin yelwataccen murmushi ya saki wanda yasa Ishmah tsaida kallonta kanshi iya tsawon zamanta dashi bata taɓa ganin irin wanan mashahurin farin ciki a cikin murmushinsa ba kalamansa take juyawa na sharaɗin mahaifinsa akansa cikin ranta take jujjuya kalaman.

Gyaran murya Yah Abana yayi tare da ɗan zamowa ƙasa ya zauna bisa carpet ɗin dake wurin cikin girmamawa ya gaida Addawa tare da cewa.
"Ki gafarceni a bisa hukuncin da na yanke kan Abbana, na kuma gode da kulawar da kika bashi, Allah ya biyaki da mafi kyawun sakamako. Ki yafe min ki kuma samin al'barka, dan darajar Manzon Allah".
Cikin murmushi mai cike da tarin jin dadi Addawa tace.
"Ba komai Muhammad ai dama rayuwa ta gaji haka, kuma komai yayi forko zaiyi ƙarshe".
Daga nan suka fara gaishe gashe, shi dai kam Tajj tamkar zai koma cikin iyayen nasa.

Ethiopia cikin kwaffa Mom Amal tace.
"Nifa tunda Malam ya tafi bamuyi magana ba, ko na kira layinsa na Saudia baya shiga.
Sai in ta Whatsapp na kirashi yana online kuma bai ɗaukaba, gsky na fara shiga ruɗani anya kuwa Malam Umran ya tafi?".
Cikin sauƙe dogon numfashi Kabeeru yace.
"Nima nayi zaton nan domin naga makar akwai abinda yake ɓoɓɓoyewa".
Cikin sauri tace.
"Kai Malam dai akwai abinda yake ɓoyewa Amman zan bincika wlh sai na gano koma menene".
Cikin lumshe ido Amal yace.
"Nifa ban damu da inda Malam yaje ba.
Kawai lamarin yarinyar nan Meymey ne nake jin tsoron sharrinta dan naga da taji tsarin plan C ɗinmu akan Afif kamar ma ta fimu zaƙuwa a kai don ko ɗazu saida ta kirani".
Cikin sakin makirin murmushi Aryan yace.
"No kada kuji komai wannan Meymey tuni na sauya mata hankali da tunani tana tare damu fiye da zatonki".
Daga nan sukaci gaba.

Qatar cikin sanyi Yah Abana ya shafa cikin Tajj.
“Zo zauna nan Abbana zo muci tare dan cikin nan da yunwa”.
Ya ƙare mgnar yana matso da plate ɗin da Ishmah ta zuba mishi cips da pepper chicken, da yaji albsa da ƙayan ƙanshi.
Sai ɗaya plate ɗin kuma jolof ɗin Couscous ne da yasha kifi da jan nama, gami da dafaffan ƙoi.
Sai kuma wani ɗan bowl mai ɗan girma da ta zuba mishi ferfesun kifi na musamman.
Hakama ta sawa Ummeyy ma.
Sai kuma su Ayeed da Ayaan.
Murmushin mai cike da farin ciki Ummeyy tayi tare da kallon Laylah da Afisha tace.
“Kuzo muci tare to”.
Aiko da sauri Laylah da Afisha suka matsota.
Da sauri Ishmah tace.
“Ummey zasu dameki da suturu musamman wanan kabaran ke tashi a wurin”.
Ta ƙare mgnar cikin tsukewa Afisha fuska da watsa mata harara.

Da sauri Yah Abana yace.
“A'a Ishmah ai yau lokacin sune, barsu suci tare, Ayeed Ayaan kuma kuzo nan muci Hamisu maza kaima taho nan”.
Aiko da saurinsu suka matso shima Hamisu cikin farin ciki ya matso.

Shi kuwa Tajj ido ya zubawa Ishmah cikin tsoron matakin da take shirin ɗauka akan Afisha na hantara da kyara.
Jin kamar ana kallonta ne yasa ta ɗan watsa mishi kallon fushi da harara  ƙasa-ƙasa.

Addawa kuwa cike da kunya ta surkai tace.
“To ni bari Inyi nan”.
Da sauri Ishmah tace.
“Addawa jirani. Zulaihat sakowa Addawa abinci da naki zo kici mu shiga kitchen”.
Sai kuma ta ɗan kalli Ummeyy cikin sakin fuska da girmamawa tare da cikar kulawa cewa.
“Ummeey me kuke so in dafa muku”.
Kai Tajj ya ɗago yana kallonta cikin mmkin yadda take sarrafa farin cikinta a kan kowa banda shi da Afisha da take musu mugun kallo na cikar fusata da masifa.
Fuska ta tsuke tare da kauda kanta gefe tamkar wacce bata son ganinsa.
Kai ya sunkuyar fuska ɗauke da guntun murmushi gefen baki jin Yah Abana na miƙa mishi spoon.

Cikin tsananin so Ummeeyy tace.
“Ishmah wannan ɗinma ai bamu cinyeba, ki huta yanxu kam”.
Da sauri Laylah tace.
“Ummmey yau kam ma ni zanyi muku girki kuji irin girkina”.
Sai kuma ta kalli Zulaihat dake cewa.
"Eh Ummey da nima ba da kina min dariya ban iya girkiba yanzu Ammeey ta koya min yau

zakisha mamaki”.
Cikin jin dadi Ummeyy tace.
“To ɗiyata kinji ko ki barsu sune su shiga kitchen.”
Cikin girmamawa tace.
“To Ummeyy na Amman zanyi muku abinci ƙasar mu Nigeria ko kala ɗaya ne ku faraci, in yayi muku daɗi sai in rinƙa yi muku irinsa”.
Da sauri Yah Abana yace
“Yau mamana kiyi min tuwo da miyar kase in akwai kayan haɗin in babu kiyi min miyar ya yakuwa yaji gyaɗa ko zogale”.
Cikin mmki Ishmah tace.
“Toh Yah Abana in sha Allah zan maka”.
Daga nan suka fice tana mmkin ya akayi yasan miyoyon Nigeria harma kase da tasan a Nigeria ma a yankin Adamawa ne tushen miyar”.

Suna shaga falon suka zaunan Addawa da Zulaihat na cin abinci ita kuwa kitchen ta wuce dan fara ɗaura miyar.

A can parlor Tajj kuwa cikin tsare Yah Abana da ido Ummeyy tace.
"Ni dai farin cikina bai cikaba”.
Da sauri suka kalleta shi kuwa Yah Abana cikin yin ƙasa da kai yace.
“Amman dai ba laifina bane ko?”.
Tana ɗan kurɓan tea tace.
“Naka ne mana”.
Murmushin Tajj yayi tare da sunkuyar da kansa.
Uwa kenan sai yau ya gane hikimar Addawa da ta nace dole Ummeyy ta zauna dashi gashi da hikimarta ta uwa ta gyara komai da haƙurinta da addu'arta da juriyarta.

“To me kuma nayi Fatima ni Muhammad da bana rasa laifi”.
Tana tsuke fuska tace.
“So nake inga yayana mata anan in ganni a tsakiyarsu a gidan dan uwansu su ganshi ya gansu suga yaransa da matarsa”.
Yanzu kam murmushi Tajj ya kasa ɓoyuwa, Allah sarki uwa.
Shi ko Yah Abana cewa yayi.
"Daɗina da Fati gaggawa, in kinyi haƙuri ai Ethiopia gaba ɗaya zai koma yaga kowa, kowa ya gansa ko Abbana”.
Da sauri tace.
“Kafin nan dai yarana su zo”.
Yana kai tsokan kifi bakinsa yace.
“Wata ƙil dai kin mance ba nine keda ikon basu izinin fitaba tun dai duk da aurensu da mazan su suna ɗakunansu”.
Cikin sauri tace.
“Tun da safe da ka shiga Wonka na gaya musu muna Qatar kuma nace su tambaya in mazansu sun barsu.

Shi ɗan uwansu zaiyi amfani da matsayin aikinsa na Pilot ya samar musu daman zuwa koda a matsayin ganin doctor zasu zo yin dan shin zasu fi samin sauƙin zuwa yau ko gobe.
Kaga matsayinsa na Doctor mai girma da asibitin sa, asalinsa ɗan Ethiopia kuma shi Pilot abin bazai gagaraba ko Afif?".
Ta ƙare mgnar da tambayarsa da sauri yace.
"Sosai ma kuwa Ummeyy in dai mazansu sun barsu".
Ya ƙare mgnar yana kamo hannun Afisha tare da cewa.
"My happiness kin gama ne?".
Yayi tambayar cikin tausayinta, Allah ya sani bazai taɓa iya jurar hantar Afisha ba, da Ishmah ta ɗauko dan yasan zafi da ƙuncin dake cikin zuciyar ɗa in itayensa na fushi dashi ko hantara.
Cikin sanyin da tunda Ishmah ta wasa mata harara ta gyaɗa mishi kai.
Sai kuma suka kalli Ummeey da ta.
Ta kalli Yah Abana tace.
"Tunifa mazansu kam sun barsu ma".
Murmushin mai sauti Yah Abana yayi wanda yasa duk suka kallesa cikin raha yace.
"To wai waya gaya Miki dama zamu zo nan ne har kike gayyato tawagarki?".
Tana shafa kan Afisha tace.
"Na gane son Afisha ya zame maka linzamin zuwa wurin iyayenta ai".
Murmushin sukayi baki ɗaya har Hamisu dake haɗawa Tajj tea.
Laylah kuwa tana miƙe mishi tea ɗin da ta haɗa mishi tare da cewa.
"Gashi yayi sanyi yadda kakeso karɓi ka sha".
Da sauri Ummeyy ta kalli Laylah tare da cewa.
"Wai ni kam Afif Laylah kam da Hamisu kam meke tafiya ne?".
Yana murmushi yace.
"Ummeyy ai bikinsu saura wata shida, kai inaga  ma bazai cikaba, kawai zan aurar dasu".
Ya ƙare mgnar da jin tamkar akwai rauni a farin cikinsa da yake tunanin bashi da ranar farin ciki kamar yau a duniya.

Cikin maganar girma da fahimtar Yah Abana yace.
"Eh to hakan zai fi, in sha Allah a Ethiopia za'ayi bikin nan kusa".
Cikin sunkuyar da kai Hamisun yace.
"Ngd Yah Abana Allah ya ƙara girma".

Ita kam Laylah tuni tayi ƙasa.

Shi kuwa Tajj fuska ɗauke da murmushi ya kamo hannun Afisha tare da miƙe tsaye tare da jawota tsaye yace.
"Zo muje wurin Ammeey ko muga me zata dafa su Ummeey".
Ya ƙare mgnar tare da janta suka nufi ƙasa.

Ummeyy kuwa da ya Abana hira sukeyi sosai dasu Ayeed.

A ƙasan kuwa, da ido Addawa ta rakashi lokacin da ya leƙa ɗakin Ishmah ganin bata cikine

yasa shi fotowa ɗan jujjuya kai yayi kamar mai neman abun da ya ɓace masa, sai kuma ya ɗan shaƙi numfashi jiyo mai sanyi tare da jan hannun Afisha suka nufi kitchen ɗin.

Ita kam Addawa kai ta jinjina tare da ci gaba da cin abincinta.

Cikin tsuke fuska ta kauda kanta da sauri ta ta ƙarayin kici-kici da fuska tare da janye idonta daga cikin nasa idanun taci gaba da motsa kayan miyan da take siyasa tamkar ba wani halitta a wurin.
“Hmmmm”.
Ya fesar da ƙuntaceccen numfashi sai kuma ya sunkuyo kan Afisha bakinshi ya kai gab da kunnenta cikin sanyi da yin ƙasa da murya yace.
“My Happiness”.
Da sauri ta amsa tana ɗago kanta tare da kallonsa da idanunta da sukayi tab da hawaye saboda ganin kallon da Mahaifiyartan tayi mata, a hankali ya ɗan jujjuya mata kai cikin sanyi yace.
“Meya sameki?”.
Sharr hawayenta suka kwaranyo cikin tsoro tace.
“Abeey Ammeyy na fushi takeyi, ban san me nayi mataba”.
Da ƙarfi ya rumtse idanunsa don jin wasu masofaffun hawaye masu ciwo na ratso mishi jijiyoyin ido cikin sanyi yace.
“Kije gabanta ki durƙusa ki kama ƙarfata ki bata haƙuri kice ta yafe miki, ta daina fushi dake tayi mana dariya”.
Cikin sauri tace.
“Abeey ina tsoro zata dakeni”.
yana ɗan turata zuwa gaban Ishmah yace.
“No je ki bata haƙuri kice mun tuba”.
Cikin ɗari-ɗari ta isa gaban Ishmah da tayi kamar bata san da ruwan tsironsu ba cikin sanyi ta tsaya gabanta tare da sa hannun ta da nufin riƙota cikin daka mata hargitse tsawa tace.
“Ke kada ki yarda ki taɓani ɓace min daga nan”.
Cikin tsananin tsoro da rauni Afisha ta fashe da kuka mai cike da firgici tare da cewa.
“Please Ammey koyi haƙuri ki yafe min bazan dake Miki oyoyo ba tunda bakya so bazan ƙara ce Miki i miss you ba tunda bakya so nayi alƙawarin bazan ƙaraba kinji kuyi haƙuri mun tuba”.
Sai kuma kawai ta durƙusa a gabanta tare da sakin maraitacccen kuka.
Cikin tsuke fuska ta sake watsa mata tsawa.
“Ke kinafa cika min kunne”.
Yah Salam shi kam Tajj tuni hawayensa ke kwaranya tausayin Afisha ya Barka mishi zuciya haka yasa da sauri ya durƙusa gabanta tare da rungumota yana shafa bayanta.
Ita kuwa Ishmah baki ta taɓe tare da ficewa ta bar musu kitchen ɗin.

Tana fita Laylah na shiga hakan ne yasa Tajj ɗaukan Afisha ya koma sama da ita domin ji yake tamkar zuciyar sa zata fashe ya sani ganin su Ummeyy a gidansa a tare da sune kawai zai sa ya danji sanyin azabar suya da zuciyarsa keyi sosai kuwa zama tsakiyarsu yasa yaji sanyi Afisha tuni ta sake wurin kakanni shima har yana murmushi.

Alhamdulillah ranar dai haka suka wuni cikin farin ciki.
A kuma ranar Tajj ya gamawa su Maryam, Rashida, Halima, da dama taxo tana Ethiopia da Zakiya duk ya gama musu shirin su akan nanda kwana uku zasu taso.

Misasalin ƙarfe tara Yah Abana ya kalli Ummeyy tare da miƙewa tsaye yana meda kallonsa kan Hamisun yace.
"Dare yayi fa, tashi muje Hamisu ya maidamu".
Da sauri Tajj yace.
"Yah Abana ya maidaku ina? Please dan Allah kayi haƙuri ku zauna dan Allah kada ka hanani samun wannan ladan".
Sai kuma ya kalli Ishmah dake cewa Ummeyy Dan Allah.
Ummeyy kuyi haƙuri dan Allah ga ɗaki nan".
Ta ƙare mgnar da nuna ɗaya bedroom ɗin dake gefen hagun daman wanda nanne turakan Tajj ɗakine da babu abinda babu a ciki, dan bai dade da canza kayan ɗakinba kuma tunda aka zubasu ko sau ɗaya basu kwana a cikiba.

Cikin lumshe ido Ummeyy tace.
"Yo ai ni babu inda zanima yau kam da Addawa na zan kwana shekara tarafa ba kwana taraba,, wata ƙil shi kaɗai zai tafi zaka ɗauko mana kayanmu ne ko Malam?".

Murmushin Ishmah tayi tare da tattare kwanukan da sukaci abinci ta aje kan dinnin table kana ta ce Ayaan ya kirawo Laylah tazo ta tattare.

Sai kuma ta wuce bedroom ɗin Tajj wanda tsakaninsa da wannan kitchen da dinkin area yake.

Komai fes a ɗakin saboda shi ba irin hargitsatsun mazan nan bane.
Harara ta liƙawa gadonshi kamar shine a kwance a wurin.

Key ta ɗauko ka tazo ta buɗe wannan ɗakin ta shiga ba wani dadti ko kaɗan amman sai da ta ƙara gyarawa tare da sauya bedsheet da blankets ta ƙara gyara bathroom kana ta ɗauko musu dukkan abin buƙata ta kawo musu tare da sa musu turaren wutan.

A can parlor kuma cikin bada umurnin Tajj yacewa Hamisu yaje.
Hotel ɗin da suka sauƙa ya ɗauko musu kayansu, sannan ya biya su kuɗin in ma akwai".
Cikin fesar da numfashi Yah Abana yace.
“Babu ma, dan dama kuɗin one week na biyasu”.
Cikin sauri Tajj yace.
“Rabonsu ne, Yah Abana”.
Sai kuma ya kalli Laylah data shigo tattara kwanu kan yace.
“Laylah tea”.
Da sauri tace to.

Dai-dai lokacin Ishmah ta fito daga ɗakin da yake ta baza wani irin Ni'imataccen ƙamshin.
“Sai kuma ta kalli Daddey dake hannun Ummeyy hannu ta miƙa da niyar amsarta da sauri Ummeyy tace.
“Barta baccin baiyi nisa ba”.
Kai ta jinjina kana ta kalli Ayeed da yake ta jan hannun Yah Abana yana cewa.
“Yah Abana zauna in zauna a cinyarka”.
Murmushin Yah Abana yayi tare da cewa.
“To my Twins ina Ayaan ɗin kuma”.
Da sauri Ayaan yace.
“Gani ta nan”.
Dariya yayi ganin shima ya riƙe gefen alkebarsa”.
Shi kuwa Tajj cikin dadin ganin yadda suka zagaye iyayen nasa yasashi miƙewa tare da cewa.
“Ku bar min Yah Abana da Ummeyna sun gaji, Yan Abana zo muje kaga ɗakin in yayi maka, in baiba a canza wani”.
Yana ƙarewa parlor kallo yabi bayansa.

Itama kuwa Ummeey bayan Ishmah tabi.

A Laylah kuma ta hauro da tray kayan tea da flacks a hannunta.
Da sauri tace Yauwa Ummey amshi kawo Daddey.
Kai Ummeey ta jinjina tare da cewa.
“A'a kai mishi”.
Daga nan suka sauƙa.